A hatsgitse ta sauko har heels din na shirin kaucewa tace wai waye yake min bokanci da sihiri agida na ?
Ta wani ja birki ta tsaya tana huci..

Ita kam banafshan Kwata kwata bataji takun mutum ba bare sautin ta kuma dama kitchen din baida nisa da dinning 2 luxury step ne kuma ya raba wajen da main falon su don haka zaka iya kallon wanda yake kitchen idan ya bude kofar

Nan kuma gas ta kunna ta riga da tasa oil a wuta alaman zata yi deep frying

Juyi nimrahn takeyi tasan ba wanda zaiyi hakan sai mutum daya amma ina take...Jin shirun yayi yawa Tuni Taje ta kashe dayan burner ta yi hannyan kichen tunda taji shiru tasan dole ne akwai mutum aciki..

Tana bankado kofar banafshan ta dago kai wani kallo ta maida mata.
Itama ta daure fuska ta sauke kanta kasa kasan makoshi tace ina kwana anty

Tace eh mm ehemm jeki cahn ki nemi antyn ki awani waje no ba antyn ki bane
Meye wannan kika kunna min agida? "wani tsubbun aka baki kizo kisa kih kashe ni ko?

Tayi mata shiru..ko sake juyowa batayi ba haka ma bata dena abunda take yi
Dama Flour take kwabawa ta rasa yadda za tayi ta motsa fargaba ke cikin ta arai
Sai yanzuma ta soma wondering ina yaya mohan din yake yau bata gansa ba ko dai tare suke? tasan idan yana nan ai bazai bari ta taba ta
Bata hankara ba taji an fincike ta sai da flour ta kife a kasa.

A dan tsorace Tace anty nifa ban san mekike nifi ba
sai tassss ta wanka mata mari bazata...

Cikin zafin rai tace
Ai bazaki sanin ba sabiida angama lalata ki tun baki tafasa ba an kona ki ya kuwa zaki san me nake cewa?
Toh Waya ce ki saka min wani abu agida na are you mad?

Hawaye suka sauko mata ta tare tayi shiru tana Kokarin zamewa ta bar wajen amma da nimrah ta shagaban ta sai abun ya wice tunanin ta

 gashi size dinsu ba daya ba kana ganin su kaga banbancin shekaru da girman jiki
Kokarin xamewa take
Tana jin nimrahn ta cahkumo ta ta tsala ihu tace dan Allah ki saake ni
Ni ki barni ta watsa mataa harara masu zafi

Ta ce bazan sake ki ba dukan tsiya zanyi miki wanda zaisa da kafan ki zaki bar min gida na munafuka kawai..
Idan ma an turo ki ne kizo kih raba ni da miji na to ki sani kece zaki fita waje muttaciya bani ba..

Kasa banafshan ta sulale tana kuka don fa sosai take jn tsoron nimrah qaurin man gyada ya sa ta mike ta kai hannu zata kashe gas din

Wani irin tumble da kayan table din nimrah tayi don ta dada razana ta tace nace kiyi waje ko..

Tace Shegiya munafuka yar iskan yarinya mutum baiya son ki ma kin nace ke wai wata irin mayya tsinanniya ce?.
Kin fice ne ko sai na kwara miki hot oil din nan?
Da sauri ta janye jikin ta amma zuciya yana hanata yin shiru. ..

Bata bata hanya ba yasa Tace ni meye nayi miki anty,..ni bance zan zauna miki da mijin ki ba ni bance miki ina son shi...why are you pestering me ...

Ta dada kawo hannu zata maka mata mari ta kauce..haushi abun ya bata tace ki fita ki bar gidan nan kiga ko zan shiga damuwar ki..just get out now.. ta daka mata tsawa.

Hawaye take kan saukewa tana rakubewa Abun ya mugun firgitata kuma nimrahn tana bata mamaki kwarai yaddda har ta iya wanka mata mari sai tayi zuciya itama ta cije..
.
Tace toh wallhy babu inda zanje kuma sai na fada ma hjy abunda kike min.....Allah ya isa min muguwa kawai

Bude baki nimrahn tayi Taace bura uba mani kike fadan hakan banafsha ?

A hatsale tace eh an fada din..toh me ruwan ki dani..you have ur husband so let me have my peace..ai nan gidan aure na ne.. ni wallhy ki fita a harkata ai ni ba yar ki bace..

Tace oh yeahhh ai dama nasan bakin kin nan na rashin kunya ne...ashe duk kinsan da hakan kika aure min miji ko? Wani wawan yunkuri nimrah tayi Bata damu da zafin pan din ba ta wasuso zata watsa mata hot oil din tuni ta hankade ta fice aguje tare da tsala ihu ...
Itama tana biyo ta da pan din sai charaf sukaji motsin mutum

Da sauri nimrah ta ajiye pan din ta tura bayan curtain ta fara masifa mai cike da munafurci

Shikam da ya shigo He can't believe what he saw banafshan ne tayi saurin komawa bayan sa ta lafe aka bar nimrahn a tsakiya

Yace meye hakan
Are you guys crazy surutun me haka...

Tace sai ka tambaye ta kafadar ta ne yayi tsayi wani ni take cewa zata buga can you believe wai ni take cewa shegiya muguwa..

A firgice banafsha Tace karya take yaya ai ita tace min sai na fita
itake ce min yar iska kuma wllhy ni ba tsinanniya bace kece muguwa asararriy..
Kuma ni wallhy kar ki sake mari na

Mamaki yasa shilll slowly ya furta what

Tace idan na mare ki zaki rama ko? Mohan Are you hearing ? kanajin abunda take fada min ko
A zafafe nimraah ta taho kansu duka tana huci irin ga babba zatayi hukunci

Mamaki ya gama cika shi
Kirjin sa har wani dif dif take ya riko ta ya tura ta gefe

Ya kalle banafshn dake makele a bayan sa
Yace Ke asje Baki da hankali sa'ar kice kike fada mata hakan..are you insane ?

Cike da dauriya tace tohta kyale ni mana.
meye nayi mata
ai da baka zo ba watsan min oil zatayi..
ni menayi mata...nan ta fashe masa da kuka
Ni ka mayar da ni gida t ni gaskiya bazan zauna ta kashe ni ba

A tsawace Yace quiet .

Tayi shiru ta sunkiliyar da kai jikin ta sai bari yake tana bulbulan hawayen tsoro shikan sa ya gane wani abu ya afku marar dadi..

Amma hakan ya cije yayi mata fada agaban nimrahn
Yace kar ta sake raina masa mata don tun kafin tasan zata shigo gidan sa yake tare da ita ..and the next time yaji tana mayar mata da magana hakan bazata ji dadi ba.

Sosai ranta ya baci,

Sosai ta kuma nuna fushin ta akan fuskan ta amma sai yayi kamar bai damu ba
Yace oya ki bata hakuri

Fuskan ta duk ya kunburo idanun ta sunyi ja Tace yayah ai baka tsaya kaji abun da ya faru ba.., .yace i don't care ..zaki bata hakuri ko sai na saba miki

Tayi shiru tana calming kanta...
Itako nimrah har da harde hannu tana wani cuna baaki irin gata nan babba irin uwar gida bata laifi.lol

Nan dai Ta sauke ajiyan zuciya tana tare sheeshkan ta tace kiyi hakuri ..anty

1 minutes bata kara ba
Ta haura sama da gudu ta fashe da kuka wanda yaji sautin na buga sa har cikin ransa

Tsaki nimrahn ta ja tayi yatsine

Ya juyo ya dubi nimrahn Yace shine ke kuma zaki watsa mata hot oil? Ita dai tasan ta boye pan din kenan har ya yarda da magaanan banfshn
Zatayi magana yace Akan me..U shud have told me that yha all need a mental home
Amma Ba agida na ba.

Baki a wangale Tace babe"
Ya daka mata tsawa cikin bacin rai "Ki bace ki bani waje i just don't have ur time now
Azafafe Ya wuce ya barta anan tasan ranshi ya baci sosai..

She just dont fully understand why baya son bata laifi agaban banafshan amma tasan yasan for sure bata da gaskiya

Amma da shike bata da kaifin tunanin sanin meyasa yayi hakan yasa ta juyo ta biyo bayansa.

Akan gado ya fada ya lunshe idanun sa tamkar ba yanzun ya shigo ba yana sauke ajiyan zuciya

gani yake kamar nimrah zata bata masa shirin sa.
Yasan idan bai tsare ta ba Zata kawo masa koma baya wajen shirin yadda ya tsara tafiyar su agidan
Shi sam baya son hayaniya abubuwa dayawa ya sa gaban sa yanzu and he neeed peace of mind definately

Wannan wai kishi ne ko hauka..Toh Why must she maltreat that girl ? Wai mata duk yadda kayi da su sai sun neme su kure ka... yayi karamin huci bai hankara ba yaji
An bude kofar dakin sa
Mutum ne a kansa

Ta kure sa da ido cike da tsiwa da rashin sanin ya kama ta

tace'mohan ka tashi kafada min akan me zaka na daka min tsawa ko dan ka auro karamar yarinya marar tarbiya da sanin nagaba da ita zaka maida kowa irin ta?

Dada lunshe idanun sa yayi yayi luff luf akan pillow baya ko kallon ta yau ne rana na farko data ya soma jin aransa lallai yayi sake wannan ai rainin wayo ne..

Haka ya mata shiru yana jin zancen nata har sai da ta kai aya tana cewa sai ta fitar da banafsha agidan.

Sanna Ya dago rikitattun idanun sa "yace idan gidan naki ne sai ki je ki fitar da ita.

Now, get out ya daure fuskan sa sosai bai taso ba tukun

Tace what?
Zata sake magana ya taso a fusace yace i said get out...

Wani bari bakin ta ya sake Tace nooo..babu inda zanje..bai jira ba sai tasssss taji saukan mari akan fuskan ta.
Bai bari ta dago ba ya haura mata da masifa irin wanda yayi mugun dadewa baiyi mata ba..

Yace ke din wacece da zan na binki a hankali kina min abunda kika ga dama?i told you to stay out of her way...damn it

Well, Yau shine rana na karshe da zan shiga tsakanin ki da yarinyar
idan raini kike so be it..

But don't you dare drag me along tunda ke dakikiyace,baki san ciwon kanki ba...sai kije cahn ki yi tayi and mind you duk abunda tayi miki ba zan taba questioning din ta bare nayi mata fada .. Ure free now so deal with ur mentality

Amma ki sani..idan raina ne ya baci dake bazaki ji dadi ba nimrah....ranta akone tace mohan u slaped me?wato bazaka saurareni ba ..ya share ta ya jawo hannun ta ya tura ta waje yayi locking door dinsa bai ko jira ta motsa ba

Tana duban closed doors din Wasu mahaukatn hawaye ne suka sauko bata ma sani ba She just can't believe it kwana biyu kenan da zuwan yarinyar nan gidan nan amma tasha mari sau biyu a hannun sa

Wanda ada chan duk tsiwa da iskancin da zatayi masa zaiyi bori yayi fushi amma baya sa hannun sa akanta

har wani rawa jikin ta yake kamar wacce ke shirin zarewa da gudu tayi waje tana kuka har ta isa shagon kawar ta jamila bata iya daurewa ba

Don haka ne ma suka shiga motar suka nufi gidan ta tare tana lalashin ta.

Bangaren banafshan ma kwance tayi luf akan gado tana kuka har dan karamin bacci ya sace ta nan ya shigo yayi tsaye a tsakiyan dakin yana binta da kallo

Hannu ya sa ya yi tapping bed din ba tare ya furta komai ba ya dawo ya tsaya ya harde hannun sa fuskan sa ba alaman wasa.

A firgice ta dan farka ta sauke masa lumshasshun idanun da suka hauro tsaban kukan da tayi..

Sai Ta dan yi shiru don ta tabbata ta kulle kofar da key ta ciki sai gashi taga wanin key din ajikin handle din ta waje

Ya ce Baccin me kikeyi ?ina ta knocking kina ji kinmin shiru

Tace ai banji bane bacci fa nake yi

yace uhumm comn get up my friend dana fada miki bacci kika zo yi anan?
Zatayi magana yace u know me wel.. bazan dauki raini ba kar ki sake maimaita wannan banzan dabiar naki
..nimrah is not ur mate dana ce kar ki shiga harkan ta why dont you listen to me?

Tace ai itace take shiga damuwa ta meyasa bazaka ce ta dena ba..
Ni walllhy bazan zauna tana mari na ba ai ni ba yarta bace
She's silently panting Dagowa tayi ta dube sa ta bata rai idanun ta sun ciko tam da ruwa..

tun da ya dawo sai yau taga ya bata rai sosai
But why dont he wanna listen ai baisan meya faru ba

Yace hmm..nidai nafada miki yau ne rana ta karshe da zan ji kuma zan gani idan ba haka ba duk abunda ya same ki anan babu ruwa na u wil deal with ur issures ba abunda zance na gaya miki kenan..

Tayi pouting lips din ta daga kan gadon murya kasa kasa tace shikenan ai ai akwai hjy mamah wallhy kuma ta sake duka na sai ma fada mata...

Ya dawo daf da ita yace kikace me?

Tayi shiru tana taro hawaye yace say it out marar kunya kawai zaki fada ma hjy mamah..
I dare you naji maganan nan a wani waje zaki ga abunda zan miki...

Wanin karfin hali ke taso ma ta kasa kasa tace oho.. nidai bance ina son wani abu daga wajen ta ba.. kuma ai bana shiga hidimar ta toh haka kawai zata na shiga hidima na kuma ace nayi mata shiru idan ta kashe ni fa..

Yace ai shikenan ai daayafi
Mutum sai shegen neman fitina da rashin ji..my wife loves me thats why she cant stand you
Gwara ita tana da dalili kefa?
Zatayi magana yace shhh i gave u a choice tunda kin zaba... zamaa dani yazama dole.. kinaji na?

hawayen ta ne kawai suka sauko tayi saurin sharewa tana kalllon sa tace naji

Haka kawai take burge sa as gentle as a pearl but shes a soft lion..

He just can deny it a duk sanda take hawaye wani irin sha'awar ta ke taso masa shiyasa aransa baya so yaga tana kuka

Jiki a nuce ya sabulle ya barta bata ma sani ba

Bangaren nimrah kuwa
Taki kwantar da hankalin ta har yakai ga ta kira lady zineta tafada mata abunda ya faru
Amma da mamakin ta taji tace taje tabada mohan hakuri kawai ta kuma ja banafshan ajiki

Kam balai,she just cant belive that tariga ta harzuka don haka shawaran jamila kawai ta dauka ta koma gidan

Vote and follow surayyahms

🍒🌺AJALIN SO🌺🍒
XPLICIT ROMANCE

WHATPAD SURAYYAHMS
Dedicated to umherny nersallah

A lokacin ana neman karfe 12 na rana don haka ko ina ya dauka da shiru musamman ma da mohan ya fice wajen aikin sa.

Nan Nimrah ta shigo a raunane ta kare ma gidan kallo ko ina tsaf alaman mayyar yarinyar har ta fito ta kimtsa inda suka bata

Tabe baki tayi tana yatsine ita damuwar kishin ne tukurum a gaban ta bata ma tunanin wani abu na rayuwan ta a yanzu

A hakan ta haura sama,da sake sake aranta wani bin sai tace ko tabi shawaran mum din ta ne kawai ta bi abun a hankali..

Amma noo ta sa abun sosai a brain din ta gani take har uwartan ma bata san zafin kishi bane. Ko ace akawo maka karamar yarinya kishiya ba shiyasa take fadan haka..

Tsaf ta gama shirya mugun tar ta taso tayi wanda zai sa banafshan ta rikice ta dena samun karrfin gwiwar magana kwata kwata agidan daga yau Sai dai kashh wani muhimmin meeting Ya daga ta dan dole ta hakura ta fice.

Ita kuwa banafshan tana nan kwance tana latsa wayar ta,sama sama take chats inda su mufidah suke mata albishir din dawowan su akan zasu zo mata washe gari

Zuwan sun ma ya dada hana qudirin nimrah wanzuwa..
Ta tsani taga banafshan tana cikin annashuwa da kwanciyar hankali..

A duk dama jiyan mohan bai wani zauna ba amma sosai ranta ya harzuka ya dada baci musamman da taga sun ware ta sun dauki junan su kamar yan uwan jini na asali.

Babu irin labarin da basu bata ba,musamman mufidan dake kokarin bata shawarn yadda zata rage zaman kadaici kafin su bar gidan haujar nimrah saura kadan ya kunce don kuwa kulle kanta tayi a daki tana maganganu..

Don ranta ace kowa a duniya ya tsani mohan baya da relationshp da kuwa sai ita kadai amma abubuwa sai dada lalacewa suke.

Ba wanda kuma take bada laifin hakan akai sai banafsha..

Da wasa da wasa har banafsha tayi sati biyu tana neman na uku,
Akallah yau sunyi waya sau biyu da anty rawiyah
Itake sake tunatar mata da nauyin aure dake kanta sometimes ko da abu ya faru idan ta tuno da maganan ta sai taji karfin giwa ya rufe ta.

Don yanzu kwata kwata ta hana ta fitowa inda nimrah take bare su hadu..

Gashi mohan ya tafi kasar hawaiii medical assist awani babban asibitin kasar,yau satin sa guda amma bata taba bari sun goga da nimrah ba.

Itama ta nemi hanya har ta gaji,ko tazo da masifan dakin ta kullum a kulle take ji gam...gashi tana tsoron ta bunka mata wuta ta kona ta ko zata mutu ace ma gobara ne kamar yadda tasha kokarin yi amma ta kasa aikatawa..

Ita kuwa banafshan bata ma takan ta,tunda ya tafii sau biyu ya neme ta yanzun haushi ma take ji da ya kira ta na musamman don ya sata girkin tarban sa gobe da yake shirin dawowa

Wani bin idan yana magana kamar ba shi ba,yaushe ya saba cin abincin ta da zai sata aikin yi masa wannan karon..
Abun ya kan bata mamaki amma wa washe garin haka ta mike sai daf yana shirin dawowa ta fara hada masa simple african dish
Vegies da crispy cocunt rice wanda yaji bushahen kifi tayi ta hade da fresh pineaple and cocunut juice
Da shike ma akwai garin daka na mata mai kyau da aka hada mata take sha sai bata damu tayi tasting ba

Dama yace mata da misalin bayan la'asar zai iso Nimrah bata nan dan haka tana gamaawa ta wuce dakin ta ta dan watsa ruwa ta fito tana shiryawa.

Colourles chappette mai qamshin beries ta goga ma lips din ta sakaya
Flair gown Violet Bowel tsadadde wanda yaji adon zaren hannu da wuya yau kam bata fetsa turare ba kayan humrahn nata kawai ta gwamusa masu sanyin qamshi da dadi tayi ras akan kujeran dakin ta tana chats...

Cikin ta ne yake cramps alaman ta kusa ta fara period dama ita a 21 days yake zagowa,
Amma da shike bai zo din ba ana kiran sallahr laasar din ta dauro alwala ta tada sallah.

Tun daga sallamr ta na fari take jin fash fash kaamar ana yakin badar da sauri ta mike ta fito ko hijabin ma bata cire ba.
Ta nufi inda sautin ke tasowa,nimrah ce a falo sautin murfin warmer abinci dake zube akasa da kuma karar zube war da akeyi a dustbin taji..

Tun daga nan ta hango ta sai aikin zubawa take yi a kitchen dustbin tana tsame baki..tana cewa..
Allah ya tuni asirin ki,kwana biyu ana labe ana shirin munafurci inba tsoro ba ai da kin wukga agidan nan kiga ko bazaki kwashi gashin ki ahannu ba.

Watoh anji zai dawo har an nannaka masa kwaban kwale..tayi kamar zata guntsuro amai,alhalin qamshin abinci ke buga ta
Tace

Ai duk wanda yaci tuwo dani miya ma zaisha nafin karfin munafurci
Badai miji na yaci barbade ba,god forbid...

Shiru banfashn tayi ta harde rai tana kallon haukar nata harga Allah ranta ya baci duk wahalan da tayi ta dafa abincin shine zata sa mata shi a dustbin?

A zuciyar ta Tayi niyyar gasa mata magana mai zafi.. amma sai taga bai dacewa tayi magana acikin fushi ga shi dama anty rawiya ta hana ta shiga damuwar ta.
Tana juyi suka ci karo da shi,..ganin kallo daya bita da shi ya sata taji wani annurin sanyi aranta.. Lokaci guda hawaye suka taru a idanun ta gwanin tausayi...
Sai da tace sannu da dawowa ta wuce ta haura sama sannan nimrah ta hankara ta mike tsaye ta gansa...

Dan sosa kanta tayi Tace ohhh babe har kadawo...bataso da yaga tayi hakan ba

Yayi karamin tsaki bai kula ta ba ya biyo bayan banafshan..

Ita kuwa Haka kawai taji wani iri zafin ne ya dada karowa a kirjin ta data gansa...
Sai ta rafka uban tagumi tayi zugum har ya bude kofar ya shigo..

Bai sake handle din ba ya kure ta da ido yace wai meye faru ne,..tana shiru kanta ma ta juya ta dena kallon inda yake haka kawai taji tana fushin da bata san ta ina ya bullo ba..

Wayar sa ya ajiye akn mirror ya karaso daf Yana kallon ta,tayi masa kyau sosai duk dama bata son cika kwalliya amma komai tayi na burge sa....hannu yasa gently ya kamo nata cikin nashi
A Kullum hannun acikin jan kunshi yake ya dan murza kadan yana shafawa sai da taji tsigar jikin ta ya motsa.
Yace hey,magana nake miki kike juya min baya ko?
Sam bata so yayi mata tsawa sai ta daure ta juyo suna hade ido ta sake masa wani irin sasanyar kuka mai kashe jiki. .
Ya gaji sosai amma Bai san sanda ya jawo ta jikin sa ba ..yace toh yi hakuri ki fada min meya same ki? Kunyi rigimar taki da kuka saba ko? Banace ki fita harkan ta ba to meya kaiki adame yafada...Cikin sheshekar Tace ah'a fa babu komai...ya dada matso ta daga ji tasan baya jin dadin kukan nata sauke muryan sa yayi cike da ladabin lallashi yace to meye,..ta dan turi baki Tace kawai nagaji ne,ai kace zaka kaini schl kuma ni kullum kenan a gida adaki ko hjy ma tace kar su mufida su sake zuwa min dayawa toh ni ya zanyi..ta dan sake makale hawayen tana boye asalin dalilin ta na jin haushi
Yace shine dalilin naki are sure ?
Lafewa tayi ajikin sa Tayi shiru abun ta
Shi duk ya fahimce ta amma mamakin yadda take kokarin nuna maturityn ta wajen boye magana yake duba.
Ai yasan tasan yaga abun daya faru yanzu kuma ya sake tambya..

Tabe baki yayi yace,kinga na gaji da shagwabn nan naki na dauka ma wani abun ne,.. yayi karamar furzan iska ya mike tsaye,..
Get up and come with me....ya fada yana kallon tsakar idanun ta

Yace zan fa barki anan tazo ta same ki ku cigaba.
Ba musu ta mike ta shiga bin bayan sa..

Nimrah dake jigilan jeka ka dawo anan har taje dakin sa taga baya nan faisal ne ya shigo da karamin trolleyn dinsa
Gashi bata so taje dakin banafshan tasan bata aikata dai dai ba daga coridorn ta ta tsaya tasan daga nan zata kalle kofar dakin hakan kuwa ta shagala da sake sake mai tatare d abakin kishi

Har suka wuce bata lura da kyau ba Wulgayar su tagani,
A hujajn ta biyo bayan su
Shikuwa yana shiga da ita ya sanya ma door din securyt doble tap lock,yadda ko an buga bazai ma ji ba.
Ita kam banafshan Zama tayi gefen gadon sa,

A yadda ya bar dakin haka yazo ya same sa,har sai da ta dan ji kunyar yanayin amma shi bai damu ba,

Wanka yayi kokarin fadawa bai takurata ba
Anan kuma nimrah ta gaji da kira da bugu har ta koma site din ta tana jeka ka dawo hankali atashe.

Yana zaayi yakai ta dakin sa..ai ance masa kar ya taba ta,ko zata kira ammy ne ta hada masa munafruci?
Wani zuciyan yace mata noo,sam bata so ayi scolding dinsa bare yaji haushi da ita shegiyar yarinyar zata kara
A hakan har tayi tunanin ko da sannun ta taki reacting data zubar mata da abinci don mohan yagani..

Kiran jamila ta dake yi ta pumpa ta ta cika dam

Ita kuwa banafshn ganin ya dada bai fito ba yasa ta dan fara kimtsa wajen tana ajiye masa komai a mazaunin sa.

Ta kintsa komai sai da ya rage da agogon da ya cire ne da wayar sa agefe

da shike irin nata ne sai ta dauka ta dan lume akan gadon nasa ta bude ta shiga latsawa..

Gallery ta shiga tana kallon pics mafi akasari hotunan da ya shafi wajen aikin sa ne,haka kawai

taji dadi aranta da bataga hoton nimrah ba sai datakai kusan rabi ta tsamo pics dinsa yana zaune a office a chan russia sanye da light brown suit bakaramin kyau yayi ba,kallon sama sama tayi tayi scrolling sai ga pics din grduation dinsa da sauran mutane daga nan tafara cin karo da hotunan nimrah,

Ba shakka lokacinda take zuwa masa ne,most of them da nity akayi su,wasu ma babu kyan gani,..haka kawai ta tsinci kanta da jan tsaki Tana maimaitawa
A karshe ta ci karo da nashi shi kadai sanye da farar rigan armless na puma da three quater sa fara ..hannun sa yasa wata kafurar silver rolex yatchxii a idanun sa kuwa wata luxury designer ta sun glasses na Giorgio armani ya sa
yana tsaye abakin wata hadadiyar beach,haka ta rinka juya hoton
Ta kalla ta sake kalla,domin kuw aba krya yayi mugun kyau a hoton komi daga siffar sa na haddaen namiji awajen ya nuna ta yadda idanu bazasu iya kaucewa ba ..

Ta shagala don daki daki take binsa da kallo kamar wacce bata taba ganin sa ba,sanyin hannun sa akan fuskan ta yasa ta dan firgita zata juya taci karo da wet chest dinsa a daf fuskan ta yayi mata karamar rumfa da nauyin sa,.har ya fito bata sani ba shine ya karaso yaga me take kallewa awayar nasa....bata iya cewa komai ba tsaban bugun zuciya ayayin da ya karbe wayar ya kalla yace hmmm,tabb ashe wata zata sha kwano.. wato har ma hoto na kika sa agaba kina kallo ko?toh Bari ta kama ki kina fallen min zaki kuwa bar mata gidan ta yanzun nan..

Wani kunya ne ya takura ta sosai amma sai tayi kokarin danne sa tana kau kau da fuska,shikuwa kallon ta yake musamman dayaga yanyin ta yana neman sauyawa gaba daya ta rude da tairon ganin sa half naked a jikin ta..

Sai ya dada tankarowa da wayo a firgice ta dafa jikakken kirjin nasa dan ta hanasa sauka akanta
Gaba daya,...amma saukar lallausan hannun nata yasa ya wani lumshe idanun sa ya sake karamar nishi....itama ta kasa dage hannun tsaban yadda gwarjinin sa yake neman dama mata lissafi,juyi mai kyau yayi da ita tafado kansa a tsorace tace yaya..moh..an..yace shhh yana dada matso mazauna ta da dukan hannun sa daya zagaye ta dashi. Bata san ya zatayi ba idan ya ce zaiyi kissing din ta ayanzu sabida har ciikin kasan marar ta sai dayayi kuru yana karan kuuu kamar mai shirin zawo..

Wani irn sexy killer lloks yake bin karamin virgin lips dinnata da shi sliwly ya sake dayan hannun sa abck side dinta yakai kan face din ta yana shafawa a lalace yana lumshe idanu shiikansa yasan ya shiga wani yanayi amma tsoron dake kan fuskan ta ya hana sa karfin gwiwar aikata abunda yake ayyanawa aransa.. Hankalin sa ya fara tashi sai ya daure ya dago zaune tare da ita ajikin sa kanta ta sunkuyar thnk gudness tasan dai da kaya ajikin ta,sai dai bata lura da hannun ta dake wasa da kananun hair din da ruwan kirjin sa ya dago ba...qamshin shower gell din duk ya gauraye mata hanci

..shikuwa wani mumunan dadi abun yake masa da shike yatsun nata kanana ne sai abun yake

mugun shigar sa hannun nata ya fara bi da kisses yana sake mata wasu mahaukatan zaafzn nunfashin shaawa akai mai rikitarwa,jikin ta duk sai ya dauki rawa slowly rikicewar nata itama ya soma bayyana ta soma kicin kicin zata sauka ..
Ko ajikin sa ya matso ta sosai yana dada shafa seducivly rough yasan towels ne da wuya ta ji kaurin full lenght din abun sa dakyau don kuwa ya tashi sosai yana neman hargowa.

Saukar hawayen ta a hannun sa ya sa ya dago fuskn ta baiyi wata wata ba ya sauke mata dan karamin peg akan lips din ta yace" wannan na miye?ke baki gajiya da kuka ne

Ta dada sake masa hawayen tana neman kwace kanta,kunya ya hanata magana,kunne ta yabi da wani irin nishj sai da ta ja nunfshin fitar rai yace hey,im really hungry me zaki bani..
Da biyu ya fadi hakan itama da biyu ta fasaara,saurin kukan ta kara tana sangarcemasa cikin yanayin shagwaba mai kashe jiki wanda bata san tanayi yana affecting dinsa ba...da kyar ta bude baki tace ai,aii aii.. babu abincin ,...
Kunne sa ya kawo dff lip din ta yace banji ba da kamar bazata amsa ba ..sai ta tsugono daf tana dan leaning ya ajiye kanta akafardar sa yace oya enajin ki...tace dama abincin nayi kuma shine anty nimrah ta zubar wai ai bazaka cin ba.

Ya tabe baki..nan ya daga ta gaba daya yace toh ya kenan shikenan dan ta zubar sai na zauna da yunwa...
Wato kinsamu nace zanci shine zaki ja min rai ko?..jin yadda yake shafo ta ko ta ina yasa tayi saurin cewa toh zan sake maka wani...yanzu..
Ta makel kele wuya ,badon yaso ba ya sauke ta ta bude kofar ta fita..
Har wani haki take duk a jike take jin kanta ta ciki amma haka ta dair eta sake komawa kitchen din ta sarrafa masa cous jollof ,in not less than 15minute ta hado ta kawo masa
Tasha mamaki dataga har yanzu yana shiri wani roel din ne ma ajikin sa laman ya sake wanka..tace ga abincin yaya...ya bita da ido
Tana ajiye ta sabkue tayi waje itama don ta kinsa kanta.

Ko cin abincin baiyi ba donkuwa lokaci yadan ja ana neman biyar saura na yamma,..
Raspberry juice mai sanyi ya kwankwada ya sanya kayan sa ya fito very gentle

Akan gado ya same ta bata sauya kaya ba duk dama ta sauya inner wears din ta,daga bakin door yace ki same ni awaje yanzu..

Kafin ta jiya ta amsa har ya bar wajen dan haka ta mike wani light purple hijab ta dako ta sakaya dan dai dai tafito ta same sa.

Tsaddiyar Bentley ce baka mai kyau bata taba ganinsa da car din ba sai yau,..aciki suka fita tare tafiyar kusan minti 30 sannan suka sauko awani maiakatan na muslim women foundation, anan akawai jajirtaccun malamai na addini mata da maza wanda uska karnta ta kowani bangaren kusan kowani state suna da makarantu dake koyar da yara da manya daki daki bisa shekarun su

Makarntar na zallan koyar da ilimin addinin musulunci ne sai dan dan kadan daga na zamanin baifi English maths da computer ba

Tare da ita suka shiga. Office din tanaji yayi bayanin sa ya siya foam din ya cikata mata,bai tsaya tanbayar ta ina take akaratu ba daga izun farko ya sa ta shikam ..

Sai da aka zo mata interview a wani aji malamin ya gane cewa tayi karatun kadan bata daiyi nisa sosai bane sannan haddan ta nanan intact alaman tana bita shi sai ya sa aka maida ta aji biyu akan washe gari zata na zuwa..

A shashin matan aure take kalar hijabin da zasu na sawa pink weeknds Morning 9 to 12
Sai sauran ranaku da yamma by 3 to 5.30pm

Aranta hakan ya mata amma taso ace ta shiga university itama ta fara karatun kamar yan uwan ta,amma da shike tasan hakan yayi niyya sai bata ce komai ba

Da kamar zai kaita gida wajen su hjy mamah su gaisa amma sai ya fasa..haka ma tana ji suka je dunes a maimtama ya siya mata duk abunda take so na ci da sha amma ko kofar gidan su basu leke ba suka bar wajen

Tun ahanya yaje gaya nata gobe zata fara zuwa islamiyar dan haka tayi adjusting time din ta har suka kai gida kow aya nufi site dinsa nimrah shiru bata dawo ba..

abincin daya siya mata da kayan kwamlashen ta dan ci kadan ta ajiye saura, yau kam ba batun shiga kitchen dama makanta take yi sai dai shi idan zai wahalar da ita yasa ta
Jin shirun yayi yawa ta kawo cewa ko ya fita ne dan zaman ta anan har an kira sallahr maghrib

Bayan tayi alwala tayi sallah sai ta sake sauya kaya zuwa three grtr gown burgendy mai short cut arms daf da sawon kafarta ..

Ganin kar sauran abinci ya fara guma waje yasa ta deba tayi waje da shi zata kaii kitchen ta ajiiye

Tana ajiyewa tana juyawa suka hade ido da nimrah d akawarta jamilah sun wani sha daurin gaba kamar hajyoyin ikko,da sauri ta kauda kai sabida bugun da kirjin ta yai mata..

Bata daka mata tsawa amma kana ganin ta kasan haushin abubuwa dayawa ke cin ta rai musamman yadda taga dazun sun lume a daki

Tace just look at her...suka mata kallo sam dakasaita da jamilan.. Tace toh annamimiya munafuka karuwan banza,mekika je kika fada masa akai na kuma?na hanaki dura masa barbade kin kai masa jikin ki ko?wai ke
me kika takama da shi ,

jamila tace fallin balaga mana ba dama suga da namiji duk sai su birkice.

Wani kakurarn tsaki ne ya kufce mata bazata tace nifa zan wuce daki..
Idan tamabya zakuyi ai sai ki je ki tambaye sa ni baruwa na.

Nimrahn Bata sha mamaki ba don ita Dama abunda take jira kenan ta amsa mata magana ta samu daman aiwata abunda ya kawo ta dan haka ta matso ta tare kofar ta hana ta ficewa,

Tana cewa kwantar da hankalin ki daga yau ai bazaki sake samun bakin maganan ba ma bare kafar zuwa karuwanci dakin miji na..yau duk karyan ki zai kare.
jamika na gefe ta nade ahanju akugu tana cewa yess
Nimrahn Hannu ta sa tana shirin zare wuka daga cutlery stand..

Nan Banafshan ta firgita zata forcing kanta wuce ta turo ta ta damko hannun ta suka shiga kokawa ,gaba daya jamila ta shiga taya nimrah tana kamo ta akan zasu yanka ta da wuka dake a hannun ta.. Ita dai bata yi ihu ko kuka ba amma ta firgita sosai ganin dagaske nimrah take zata fa iya zaro wukan ta chakka mata yasa ta manna mata cizon da sai da wajen ya shiga sosai ya lutso yaui ja jir.. bata iya daurewa ta ta fasa ihu ayayin da itama banafsha ta samu ta kufce ta sa gudu a firgice zata haura sama..hade da zafin cizon yasa nimrah haukacewa tace ma jamilan ta tsaya nan
jin shiru suke tunanin suka dai ne agidan
Wukar ta rarumo ta biyo ta dashi aguje,tayi saurin shiga dakin ta ta rufe karkatwa take har jikin ta na sanyi da kansa..

Aksa ta sulale cikin tsananim tsoro tana jiwo yadda nimrah ke zazago barazan kashe ta abakin door din idan ta ske ganin ta adakin mohan

duk tana hakan ne don ta razana ta sosai don tasan dagaske takeyi bazata taba barin ta ta zauna lpya agidan ba .ai kuma tasan karamar yarinya ce zata gaji ta gudu wata rana..har burin su ya cika

Ganin tana dada firgita yasa ta lallaba ta dauko wayar ta,bata taba dialing nunber sa ba sai ranar da shike aiki yake yi kusan ringing biyu yayi mi kyau sannan ya lura..

Maysoon?..ya fada abayyane ya mike batare da ya daga wayr ba ya fito agurguje..saurin saukowar sa yasa nimrah tayi saurin saka wukar acikin ta ta koma gefe ta daure fuskan ta tam tana surutai tana harhada magana ..

baisha mamaki ba,dama shi yasan haka kawai bazaiga kira ba,baice komai ba ya buga kofar bata bude ba gashi key dinsa na daki,hakan yasake komawa da sauri don ya dauko

ita kuwa banafshan dataji shiru bai daga kiran ba, ta shiga tara kayan ta a dan jakar ta anan ta

fashe da kuka sosai tana jin wani irin karyewar zuciya

Daama hijabin da tayi sallah ta jawo ta kwaba har yana rufe fuskan ta tsaban ta damu,yana bude kofar ya same ta a rakube agefe gwanin tausayi . .

Cikin wanin rin yanayi yace banafsha? Taji dadi aranta data ji sautin muryansa amma bazata iya jute taorn data ke ji ba,ai gidan nasa ba aljanna bace ita san tagaji don tamkar prison haka take zama da nimrah

the only time she had her peace was lokacin datake doje mata bata bari su hadu,yanzun kenan ita bata da freedom agidan mijin ta?

Duk yadda ta so ta daure ta kasa yana talalfo ta daga kasan ta fada kirjin sa ta sake wmasa wani fitinanne kuka...

haka kawai yaji ya razana da yanayin ta musamman ma dayaga yadda idanun ta suka kumburo sukayi ja...

Kafin ya sake tanbayar ta ta ce dan Allah ka kaini gida yaya...ai kashe ni zatayi ni bana so na mutu anan wajen...kaji dan Allah..ni gida nake so ta dada fashewa da kuka
ya riko hannun ta karkawa take yi sosai sai ya kasa cewa komai yana kokarin nitsr da kansa

Mutsine nimraah jamila tayi irin taje ta aiwata karyan da suka shirya zasu fada don kar ma ya saurare abunda banafshan zatace anan gaba..
Daurewa yayi bai tanbaye kowa ba daga cikin su ba,ya jawo hijabin data sa shi ajuye yace babu wanda zai kashe ki ...ya zare hijabin yace zaki kashe kanki ne? Jakan hannun ta ya watsar a kasa
Jawo ta yayi zasu fita tare nan nimrah ta sami karfin giwa bude baki tayi magana .

Mistake daya tayi data daura hannun ta zata jawo banafshan daga jikin sa..
don kuwa bai bata lokaci ba ya takarkare ya juyo ya daura mata wata lafiyayen mari sai da wajen ya yanke da silence...
Shi dama abunda yake gudun nata kenan amma yau ji yayi bazai iya hakura tana cigaba ma yarinyar haka ba
Yace ma banafshan ta bar wajen ta jira sa adakin sa. .da gudu ta haura ta firgita dan haka ta dunkule waje daya tayi shiru tana sheshka

Wani kallo daya jefo ma jamila sai da ta hadiye yawo a sukwane tabar masa gidan sa

Haka itama uwar gayyar bai kyale ta ba,

Ya budi baki yace ya sake ta ne kawai bai fada ba,amma yadda ya razana ta da kalaman sa yasa ta ta firgice fiye da yadda ta firgita banafshan da kafarta ta fice ta bar masa gidan sa

Da shike ransa ya bacoi sosai cahn sama ya je guest room ya kwanta ruff da ciki bai sake dawowa ba sai da ya tabbata tayi bacci

Washe gari dalillin dayasa bataje islamiya
Bake nan don siai kanta ya dinga ciwo da kyar da rarashi ya mata allura ya samu ya fita

Nimrah kuwa dama babbacgin tayi ma kwana tayi tana kukan takaicin rayuwar ta agidan jamila.

karshe Haka suka hakura a wannan lokaci ta shirya ba bata lokaci ta wuce offishin mahaifiyar ta.

Dama jiyan tazo maiduguri yau zata zo abuja daga nan kuma zata tafi japan
Don haka nimrah tayi zaman kashe wando full time a quest house tana jiran saukowar ta.

By 3.45 pm suka samu zama don kuwa tun da zun ta ishe ta da bayani a waya ..
ko da suka zauna step sis din lady wato hjy adama tace ma nirmah ta gaya mata asalin labarin meke faruwa agidan
Nan ta shiga rero musu abunda ya faru
Inda sukayi shiru suka hakimce Kallon ta kawai lady zineta take yi cikin ranta tace"lallai nimrah bata da lpya..'ta ayyanah da wani rin disguisting looks

Cahn hjy adama ta ce ranki shi dade..my dear sister.. ya kamata ki dauki tsassuran mataki akan yaron nan ban taba tunanin izigilin sa zai sa ya dinga daura hannun sa akan nimrah ba"
Thats unforgivable you know

Ba bata lokaci lady ta tabe baki tare da binsu da kallon basu san me suke yi ba..

Cahn Tace babu abunda zanyi masa nikam ma yayi min dai dai I wish dukan tsiya yayi mata..iskancin banza
Tayi tsaki ta mike zata bar wajen

A hargitse nimrah tace mum?

Tsawa lady ta buga tace kiyi min shiru nimrah...

Ashe baki da hankali meke damun kwakwalr ki ni kenan Kullum ina kullawa ke kina barazanan warware min
watoh duk abunda nake gaya miki akan yarinyar ba kiji ba,..shawarar kawarki kike bi da shike itace uwar ki ta bariki ko ..i told you many times babu wani kishin haukan na tsakanin ki da banafsha farasat.
What are you tryn to prove now..duk bayanin da na miki bakiji ba kO yarda dani ne bakiyi

ba?ohh watoh
Har Kin fara tunxira shi yana marin ki agaban ta and then what next?me kike tsammani kuma dama.

Sunkuyar dakai nimrahn tayi
Lady ta cigaba tace
Hmmm my instinct were right dama.. ure so worthless amma sabida kin taka babban rawa wajen sarke mini alhaj muamar acikin harkoki na rayuwa sai na soma tunanin maybe kina da amfani.

Ni nan Nafi kowa sanin tun Lokacin da na haife ki baki da amfanin komai a duniya cos ure so dull nimrah

Gashi na yi miki auren ma na barki shine har kike tunanin warware min shiri na..

Kuka nimrah ta fashe da shi ta kuma mikewa a zuciye zata bar wajen batace komai ba
Tashin hankali ne ua gauraye wajen kowa da abunda yake ji na bacin rai

Hjy adama tace habawa"Zineta Wai meye hakan ne ..she's ur only doter fa matsalan auren ta ta kawo miki
Bai kamata ice haka ba...

Tace i dont care anymore Adama...kina tunanin nace ki taho tare da ni ne dan na saurare ta?meye ban mata ba?
Mari,..duka,tazo nayi mata ko kashe ta zanyi?

I got her life...na bata rayuwa mai shegen kyau da wadata.. mijin data ke gadara da shi din ma ni na bata shi...sabida bazata iya komai akansa da rayuwan ta ba this is 4years amma har yau bata taba samo kan namiji ba?
so all this favour abanza nakeyi kenan tunda magana ta kwalli daya ta kasa dauka

Sulalewa kasa nimrah tayi ta sake fashewa da kukan takaici da bacin rai

Lady tace Ohhhh Allah!! anya ba sauya nimrah akayi wajen haihuwa ba kinsan ba haka nake ba ko adama?wannan dakikan cin data keyi ba jini na bane tasan inda ta debo

Nan anty adaman ta mike
Tace pls calm down zineta Allah ya huci zuciiyar ki...nimrah bata kyauta ba amma ai hannun ka bazai rube ka cire ka jefar ba..

Can we please try and be a family for her na yau kawai..mmm
Kiyi hakuri ta sauke murya tana rarasshin ta.

Da kyar ta dago ta dube ta tace this is the last time da zan saurare ta.
Damuwa ta ba auren ta ba muamala na da alhaj nake dubawa.

I need him musamman yanzu da na sa siyasa ta agaba
Anty Adama Tace haka ne kuma bazamuyi wasa da wannnan ba
Nimrah maza ki durkusa ki bada mahaifiyar ki hakuri

Tana cikin wani halin bakin cikin amma haka ta rusuna tace im sorry mumy dan Allah ki taimaka min...wallhy komai ya lakce mohan bana gane masa ko kadan i swear

Lady Tana shiru don ko kallon ta batayi ba
Fada anty adaman tayi ma nimrah akan kar ta sake haka ya sake faruwa...tana amasawa cikin ladabi idan kaga ganta sai kace baa ita bace

Nan suka zauna
Lady tace a baya namiki bayanin komai na tafiya dai dai ta wajen sihirin ki akan sa,fannin yarinyar kuma is all done tun ranan farko na fada miki ba yarda da shi zata yi a matsayin miji ba tunda ta rike akanshi iyayen ta suka mutu..komai akan akalar mu yake musamman da uwar mijin take da nata fannin kalubalen da zamu latsa to our own advantage

Shiysa Nace kar ki shiga damuwar yarinyar sabida na samu daman shiga da dabara na ta karshe wanda zai kawo karshen dukan matsalan nan
Da nace ki takura ta bance ki takura ta da hauka ba..

Son banza da wofi dakike masan ai ya dace mashi kadai zaki yii haukar inkinsan ke macece
Shiyasa nace babu kishi
For god sake katuwa dake sai na fada miki yadda zaki takura karamar yarinya ta gudu a gidan ta?

Ko sake kashe ta zakiyi ki jawo min wani jafa'in?
I expected to use ur poweer and brain as a grown uo woman

Ni da kike gani na nan Mahaifin ki bai taba kaunata ba infact sharri nayi masa na karbe rayuwan sa daga hannun wata ya macen dayake ikirarin yana son ta tana son shi.

Duk taurin kai da izzan mohan ko kadan bai kamo na mahaifin ki ba,nasan yana da wacce yake so nima kuma ina son sa
Amma bansa hakan a gaba na ba

Na aure sa da karfin kwalwarta da iko na bada kishi da hauka ba

Haka kuma ya mutu kaskantace awaje na.
Ni ban masa sihiri ba sabida nasan na isah mace.

Muddin kina so ki dawo yata nayi alfahari dake Kema hakan nake so ki zamto.
Don wallhy nimrah kika sake wani fanni daga plan dina ya girgza wajen alhj muamar da hannun zan kashe ki

a firgice nirmah ta dago ta dube maman nata wanda bau ko shakku a zance nata

Tace Abu daya zakiyi yanzu
Ki koma ki ajiye kan haukar da kika fara
ki bashi hakuri..yarinyar zaki ja ajikinn ki
Play ur codes cikin salo har ki samu ki fitar daita agidan da bakin ciki wata rana and that day i shud persnaly plan her dath clean and natural

kinga ba wanda zaice kin kashe ta amma yanzu dakike haukr ki ko ciwon kai tayi mohan and his dad wll definatly hold you responsible and i wll not spare you too..
Da muryn barazana mai cike da shauki lady ta karasa maganan ta

A hankali ta dago tare da sauke ajiyan zuciya tace
I promise you mum daga yanzu i wont eva disapoint you wallhy nagane kuskure na

yadda tayi magana sai ta basu tausayi hjy adaman tace good girl maza tashi kike ba zama ai da zafi zafi ake bugan karfe

haka tayi msu sallama ta bar wajen

Sai dai bata iya komawa agidan ba sai da ta nitsar da kanta da maganin da alluran bacci sannan ta yanke hukuncin

Ita kuwa banafshan Yau kam tun da ta tashi taga sarai yana binta yana lallabata sai ta samu damar zuwa gidan hjy mamah don ta cinye wunin ranar anan

akan idan ya dawo daga aiki sai su taho tare ,
Taso ta fada ko da kadan daga abunda take fuskan ta amma yadda suka ishe ta da zumudi da kwainane irin na tsoffin yasa ta kasa maganan komai ba sai kawai ta bisu suna faman hidaman surutinn su islamiyna da yasata kawai ta fada ma hjyn mamah suka sa albarka

Dama yau kafin su fito yaya mohan dinta ya bata sabon laptop mai kyau na apple,sain ya kasance tun zaman su anan sadik da ahmed suke tura mata films da abubwan da zata bukata wanda zasu debe mata kewa

Bai xo ba kuwa sai bayan ishai lokacin gidan ya fara shikar ta har bata so ta bishi,..
amma hakan ta hakura ,suka tsaya gidan ammyn sa nan ma sama sama suka gaisa ya wuce da ita gida .

Dama cikin ta na murdewa ta dauka ma period yazo ne sai taga baizo din ba kayan baccin ta mai kyau ta sakaya zata kwanta ko kyakwan juyi batayi ba saiga sallamr nimrah

vote and follow surayyahms

🌺🍒AJALIN SO🍒🌺
XPLICIT ROMANCE

Watpad SURAYYAHMS
dedicted to umhny

PAGE25

A firgice banafshan ta mike daga zauna tana zare ido dan harga Allah tsoron ta take ji.

Itako nimrah Tana lura da ita sai ta sauke wani boyayyen ajiyan zuciyan na munafurci tana isowa kusa da sauri banafshan ta mike tsaye zata koma gefe nesa da ita..tace'ni ba wani abu na zo nayi miki,magana kawai zamuyi ...ok? Ta daure dai ta fada adan saukake

Yadda tafada ba yabo ba fallasa yasa banafshan juyawa ta kalle ta cike da shakku batace uffan ba

Sai ta matso kusa kadan tace,ni rashiin kunyar ki dama yake hada ni dake amma ya kamata ki cire komai aranki yanzu kiyi hakuri da abunda nayi miki.. Kowa ya zauna akan matsayin sa Kina ji na?...mamaki yasa banafshan tabe baki tana kallon ta irin anya ba mafarki nake ba.

Tace ina miki magana kinyi shiru,ni fa ba sa'ar ki bane da dan kin ga nazo ina baki hakuri zaki raina min wayo

Anan tace ohh ai ni ban san hakuri kike bani ba fa.

Aranta tace what? Take ta danne bacin ranta Tayi murmushi mai ciwo tace toh nafada miki yanzu.
Let's be cool ..bana son kuma ki kawo min wani raini ,nan gida nane ..miji ma nawa ne. .ure just like a little sister to us don haka ki kama kanki ai kingane me nake nufi ko.

Wani kallon kasan ido banafshn tayi Kasan makoshi Tace ok.

Da kyar nimrah ta wearing fake smile tace toh sai da safe ta fice.
Ta juya har da jawo mata kofa

Durus banafshan tayi har tana leken ta don kuwa bata gama yarda da nimrahn ce take fadan haka ba..
Ashe ta san ta girma ni kuma karama ce take wannann haukar?...ta tabe baki.

Gadon ta haura ta jawo system din ta. . Series din into the badlands ta fara sakawa tana kallo

Nimrahn ke tahowa zuwa dakin sa don Kafin ta zo sai da ta dade tana shan ruwan sanyi tana huci..ba al'adan ta bane sallama don haka
Tana turo kofar ta hange sa akan gado ,daga shi sai sweatpants yayi luff luff kamar mai bacci.

Ganin sa hakan ma Wani dadi taji aranta,only god knows how much she loved him amma ta kasa gane me takee ciki yanzu..

Wani fuskan shagwaba tasa wanda ko karban surar ta baiyi ba dama kuwa gashi ta tsani saka atamfa amma dan tasan yafi son tana saka irin su
Yasa ta saka yau.

Jikin sa ta karaso direct ,ta dan lafe abayan sa tace mohan baby...ta sako bakin ta ramin kunnen sa tace nasa kanaji na..im sorry baby....dan Allah kayi hakuri..

Ko motsi baiyi ba bare ya juya ya kalle ta..

Haka tayi ta maimiatawa tana murkususu ajikin sa amma shiru..
Sanda ya ja mata tsaki ma tasan yana jin ta,gaba daya sai taji ta damu kenan yarinya zata raba ta da shi kenan ko me?

Ta gama mancewa yasan halin ta na sa fuska biyu, tun akan aysha ya gane cewa nimrah bazata taba yin gaskiya arayuwan ta ba

Nan ta rikice Har da dan fake tears din ta Tace i promise mohan alkawari nayi maka yadda kace hakan zamu zauna..pls don't turn ur back on me hubby,..yana shiru..tace am sorry ...nice bani da gaskiyan but you know i cannot leave witou you jiya fa ko nema ta bakayi ba kenan ka dena damuwa dani? Hannun ta ya ture ajikin sa...ta fashe masa da kuka nan ya tashi ya mike kamar wanda zai bar mata dakin ko alaman wasa babu a face dinsa..

Da sauri ta taro sa suka tsaya tare duk sai tabi ta rude musamman ma daya dage kansa sama irin bayason ma ya kalle ta bare yaji tausayin ta,yana motsawa tayi sauri ta fada a bare chest dinsa tana wani numfashin kuka mai rikitrwa tana shafa sa cikin wani yanayi...

Haka kawai yaji daban sai ya fincike jikin sa yana kokarin tura ta hefe ,ita sam bazata iya jure fushin sa ba yanzun kam dagaske ta fashe masa da kuka mai tsanani tace haba mohan duk akan yarinya kake wulakanta ni, ai kasan bana son kishiya ne im just tryng to cope with her..na

dauka zaka fahimce ni..

Ya dan kalle ta,yace pls let me be manah, .ba kin gama maganan ki ba,to ni bacci nake ji..goo ..ya bata rai ya juya mata baya.

Gashi Ta tsani yana mata shirun nan gwara ma ace da zagin ta yayi ,...wani tunani tayi sai ta sauya fuska kalar tausayi A sanyaye tace mohan na bata hakuri fa..duk da haka fushin zaka cigaba dayi?

He was shocked to hear that amma da shike ya juya baya sai bata ga reaction dinsa ba

sai tayi shiru gwanin tausayi kalar munafrci nan ta goge tears din tace to shikenan kayi baccin gudnite..

Tana juyawa ya kamo hannun ta yace dagaske kike kin bata hakuri?

Wani irin bakin ciki taji ayayin da bakin ta ya kasa budewa tana kallon sa ...hawaye ta sauke ta gyada kai alaman eh kamar ba ita ba"

Yana duban ta Yace toh meyasa kika bata hakurin for what?bake bakiji ba

Tace,noo.. i really love you mohan.. ba abunda bazan iyayi akanka ba..ni bance zan iya danne kishi na ba... i just realised ive been childish with her but im sorry ni kar ka yi fushi dani..

Yadda ta marairace ta shanye idanu yasa yaji tausayin ta ya fara taba shi

Sai ya sauke ajiyan zuciya yacee ,comon zo nan.. ya jawo ta zuwa gefen gado suka zauna Hawayen ta ya shiga sharewa a tsanake ya takure ta da rikitatun idanun sa dake kashe mata jiki cikin sanyin murya yace can we talk now?

Ta gyada kai,kasa ya dawo ta gaban ta sukayi locking idanu,hannun sa yasa a fuskan ta ya shafo ta yana kashe ta da killer looks irin wanda take matukar kauna..

Ashe gaskiyan mum ne,namiji sam ba acimma masa da hauka...

Nan ya shiga mata nasiha cikin salon yaudara duk yakashe ta da kalamai masu zaki masu taba kwakwalawa.

burinsa kar wani abu ya dame banafsha agidan

A cewar sa ta daure ta rike banafshan kamar yadda zata kula da karamar sister sa,shi da kansa ya mata alkwarin bazai bari ta raina ta ba..and he promised to love her in which other way..cewar sa duk rayuwn soyayyr data ke so tayi da shi zai mata muddin bazata maimaita

abubuwan datake yi ba kuma zata rike girman ta na babba agidan..

Duk dama hakan ba ra'ayin ta bane,amma yadda taga yana lallabata yana sauke kai yana sumulmula ta sai tasan kawai bata da wani mafita sai wannan din..

Hannun ta ya rike yayi kissing yana zuga ta da cewa yayi missing din ta kuma shii dama ita kadai ce matar sa da yake so
ai banafshan batada matsayin ta wajen sa tunda ma taji ai ammy tace ba shaanin aure atsakanin su..sai yauki take tana lalacewa da rigima ita a dole tayi babban jihadin zata zauna da kishiya..

Duk dama ta nanata cewa daurewa kawai zata nayi..shidai haukar ne dama baya so.
A game da zaman sun Ta zuba dokoki iya dokoki amma baice komai ba

Tunda ma ya jawo ta suka shige bathrum tare sai ta mance da komai yadda yaje mata ana sai ji take kamar ita ce matar sa kwalli daya a duniya

...dama masifa ya hanata sake ranta ta bashi hakkin sa tunda ka kawo banfshan baifi sau biyu ta barshi ba..

Shi kuwa yau din dagaske yayi don kawai ya gwada mata yana tare da ita kuma ya fahimce ta akan kishin nata...
Ranar baccin da tayi har tana wangale baki tana birgima..

Haka rayuwar su ta fara kasancewa ita kanta banafshan tasha mamakin yadda nimrah ta rike kasa wajen jan girman ta da baza mulkin ta cikin salon munafurci...

tun tana yi a hankali har Ta fara bankedewa tana mata masifa da iko kamar ya da uwa

yadda take bata oder yi kaza bar kaza gashi yanzu direct sai ta shige mata dakin ta ba excuse kamar yarta haka zata tsaya akan ta tana mata magana da sunan ita ce babba

abun sai ya fara bata haushi..

Ita dai zata tashi ta kimtsa gidan normally kamar yadda ta saba kafin taje schl da yamma ko da safe..,gashi har da na wulakanci yanzu ko cup nimrah bata dagawa idan tasha ruwa
Kuma idan taje ta dawo ta samu ba adaga ba haka zata shiga kwalla kiran banafShan akan tazo ta daga mata dattin nan a gidan ta.

Sati daya ne kacal amma A hankali banafshan ta gane cewa nimrahn bata wani shiryu ba sabida a idon mohan bata mata wasu abubuwan..

Ita kanta nimrah ta gaji amma da shike taga mohan yana kula ta hakan sai yafi mata komai ba

Gashi sau goma idan banafsha ta fito zataje islamiya hakan zata ga ta nannade shi a falo da wasu banzayen kaya tana kissing din wuyar sa tana shafa shi ko da bai kulawa zata nanike masa yadda kasan ko yaushe take timing saukowar ta

Da safe kuwa Har wani speacial coffee time ta bude musu da safen kafin suje aiki

Banafshan Har ta gaji da halin ta ta dena gaishe ta,
musamman idan taga suna tare a wannan yanayi...

Amma duk da hakan hakan nimrah zata rinka complain dai dai da lokaci guda ta wulga zata fara cewa baby kaga ko gaishe ni bata yi ba...wata rana ya kula wani bin shima cewa yake aini ma ba gaishe ni tayi ba...

"Tace tab ai kuwa bazamu zuba mata ido tana rashin kunya ba,shikuwa idan yana so ya rufe mata baki sai ya soma tambayar ta tayi sallah kuwa? yasani sarai idan ya kawo maganan nan bazata amsaa ba sai ta tashi ta shige ciki..

Ya rasa meya yake rabata da son yin sallah yayi maganan shikam har ya gaji..

Yau ya kasance watar banafshan biyu da tarewa agidan,fazila ta sauko daga uk adaren jiya don haka yau ita maryam suka kawo mata unxpected visit

murna kamar zasu hadiye juna sai surutu suke a falon da shike ma babu kowa ranar jumuah ce..

Suna ta tsokanan ta musamman da suka ga yadda ta dan sauya tayi fresh,
basu san duk damuwa bane acike da ranta

Subhallah Banafsha!!!!! hjy ta kira sunan ta a rude tayo kanta,

Amai kawai ta keyi kamar hancin cikin ta zasu biyo baya

..da kyar take furta wayyoh Allah ciki na,nannnah ciki na kemin ciwo'
Hjy tana ta kokarin riko ta tana zarmewa
Cikin wani fitinanen kuka ta sulale kasa tana Kara kakari mai tada hankali.

Tsaye mahnoor ta yi tana kallon su,kirjin tane ya shiga bugawa ta karaso kanta itama tana kallon ta..Banafsha na kuka hjy mamah gaba daya ta rude tana tambayar ta meke damun ta?

ganin abun yayi tsamari hjy mahnoor tace bari a aika doc ya zo ya dubata ko dai abincin ne yayi irritating din ta,?

Jin ance doc Banafsha sai ta farga"ai yayah mohan yace mata kar ta sha wani magani ko allura shikadai yaxe zai na duba ta, tuno da hakan yasa ta dagowa a
A wahale ta shiga
Girgiza kai wanda yayi dai dai da isowar hjyn birni daga step ga nimrah ta bakin main door,

Dukan su kallon wajen suke da alaman tambaya afuskn su,.

dama ita hjyn birni tafahinci wani abu,amma da shike tasan yadda su kansu suke shgwaba ta sai ta basar...

Cewar datayi kar a kira doc,yasa hjya mahnoor ta shiga yi mata fada,nidai bazan dauki wannan Sakalcin ba kikayi wasa har asibiti zasu kai ki .

Kukan ta na daga ma tsoffin hankali sam basu so sugan ta a wani hali,itako nimrah tsaki kawai takeja tana tsaye uffan batace musu ba,

Tashi ki zauna anan kafin doc ya iso. ke Nimrah kirawo masu aiki suzo su kimtsa nan wajen...
Hjy mahnoor ta bada oder.

Ita kan Banafsha kuka take yi a wahale tana nishi

Cike da zurfin nazari hjyn birni tace Ah ah,tsaya tukunna,zo nan Banafsha ta kwace ta a hannun

su tana kare mata kallo,hawayen fuskan ta ta soma share mata
Cikim lallami tace auta?
Yaushe kika fara wannan aman ne,?sheshekan kukan bai sake ta ba haka ta daure tare da sauke ajiyan zciya tace Hjya,ai tun ranar Ne
,....abincin yana daga miki zuciya ko ?
slowly ta gyada kai..

Anan gaban kowa ya fara fahimtar ina hjyan birni ta dosa.

Automatically Nimrah taji not din kanta suna kuru zasu kunce

One time hjya mahnoor itama ta saka dukkan attention dinn ta kansu tana so taji karewar zancen

A nitse hjyn birni tace "To meyasa baza ki bari a duba ki ba,ko mohan ya sani ne?

Ta gyada kai, cikin shagwban kukan nata ta furta yaya yace fa kar nasha wani magani,ai shi yace in bani da lpya na gaya masa zaiyi min maganin da kansa.....

"Ok mohan yasan kina amai?kanta a kasa tace eh yasani

Wani shiru ne ya dauke wajen
,dukan su fuskan su dauke da wani intense feelings na suspense

To cut the suspense don kowa ya fita a zargi,.
hannu hjy mamah ta sa ta dago ta tsaye ta tsura mata ido tana Kare mata kallo "auta na Gaya min gaskiya meke damun ki?

Shiru tayi jikin ta ya dau rawa sosai ta kasa hada ido da ita.

,...cikin wani yanayin tashin hankali mai zafi hjy mahnoor ta yunkura zata daka mata tsawa

,hjy mamah tace mata pls don't
..basai an haura mata ba A nitse zata fada mana komai

Nan Hjy mahnoor taja bakin ta tayi shiru

Banafsha nace meye ke damun ki, .. ive been noticing you ki kayi min karya yanzu zan sa doc ya duba ki..

Daurewa tayi ta runtse idanu,sai da taji hjyn birni ta dafa ta a hankali sannan ta bude ido wasu mahauktan tears ke saukowa
Ganin idon kowa na kanta sai ta dada rikicewa

,.murya na rawan
Tace nan..nah..nannah,uhmmm.....uhmm uhmm....dama yaya mohan ne,..
Yyah moh..an

"cikin wani irin salon tashin sense hjy mahnoor tace mohan din Yayi mike me?ana tambayr ki ciwo kina kawo maganan mohan will you stand straight my friend ?wai meye haka.

kuka ta fashe da shi dan tsoro"
,sukuwa tsoffi tuni suka gane kan zancen kallo kallon sukayi ma juna cikin ransu kamar su balle suyi guda dan farinciki..

Jawo ta jiki hjyn birni tayi cikin lallami tace yi Shiru abun ki..kinga dena kukan nan,baki da lpya kuma Shi yace miki kar ki fada ma kowa ko?
bata san sanda ta gyada kai ba

A birkice nimrah tace what?

Wani bala'ein numfashi hjy mahnoor ta ja tace ai sai ki fada mana muji mumah wani irin ciwo kikeyi wanda anan gidan ni uwarsa ma bazan ji ba...ni na haife mohan,so bawani sirrin da zaiyi dake ya kasa fada min u better say it..

Hjy mamah ta riko hannun ta,dan sosai tsoro ya bayyana a fuskn ta
"...gyada mata kai tayi akan tafada kawai.. Da kyar ta taro confidence,... Tace kiyi hakuri nanna,dan Allah kakakkiyi fushi dani wallhy yaya ne yace min kar na fada ma kowa kuma nima bana sooo,ai shine yake yi min kullum

wani kukan ne ya sake kufce mata hjy tana bi tana gogewa cikin murmushin jin kunyar kalaman yarantan nata

.."ciki kike da shii ko Banafsha?

,kunya da nauyi ya sa ta Ta runtse ido ta kasa amsawa,..

Comn speak up autar hajya,yar gata ta,meye ne zaki boye min ne auta na?

ajiyan zuciya ta sauke cike da kuruciya ta shiga i,'i na a nitse tace hjy dama yaya mohan ne yace min wai ina da ciki.

"kina da ciki? Hjy mahnoor ta furta a firgice'

"Alhamdulillah!!!!
Tsoffin suka fada a tare Suna mika hannun su sama.

Wani luiii idanun nimrah suka dada yi,wuta ne ya kama ta cikin brain din ta yana ci bal bal..

Ji tayi kamar za tayi collapsing amma ganin yadda hjy mahnoor ta shiga shock din dayafi nata sai tayi maza ta taro karfin giwa ta koma jikin ta

..muryan ta na rawa ta dan rike ta tace mum lpya kuwa?...mum please relax.. Wannan ai abun farin..ci..ki ne ta karasa a shakure

Dagowa hjy mahnoor tayi da wani mugun harara zata warware musu masifan dake cin ta,sai charaf suka hade ido da mohan a gefen alhj muamar suma sun shigo..

Shikam Kallo daya yayi musu dukan su Jikin sa ya bashi labarin abunda ya afko..

So yake su hade ido da Banafshan amma taki ta kalle sa,su hjyn birni kuwa sai lallabata suke suna zuba mata dadadn kalaman albarka masu taushi da masu kwantar da hankali

,.take taji karfin gwiwa da sanyi a ranta ajiyan zuciya take yi slowly suna shafa kanta cike da shaukin nuna farincikin su

Hjy mamah nan tace ma hjyn birni kai ta ciki ta huta,abun datake so sai abata taci
Sannu kinji Allah ya raba ku lpya

"ba musu hjyn birni tace..toh ta riko hannun ta suka taho ta gaban mohan da mahaifin shi murmushi hajya tayi mai tafe da hawaye tace Allah yayi ma rayuwar ka aminci da albarka lamido na..im very proud of you today more than any other day

,Kasama mana farin ciki,ta juyo ta kalle Banafsha data sadda kai kasa a gaban su..

"sai ta dan shafa fuskan sa tace insha Allah kaima acikin ta zaka dawwama.

"Cikin sanyin jiki ya amsa da ameen ummah na gode.."murmushi tayi dan ita kanta tasan hardly yake kiran ta da wannan sunan,

..wani dadi ta keji in ya fadi hakan..
Kallon su yake har suka lume

Sai dai baya cikin hankalin sa duk hankalce yake da kallon da uwar sa take masa
Ko kadan bai damu da yadda jikin nimrah ke nuna karkawan sa a fili ba

Alhj da bai san komai ba,yayi gyaran murya yace mamah meyake faruwa ne?

da fara'a hjya mamah ta taso za tace ai mun samo kar...u..w

Hjy mahnoor ta sa ihu a hatsale tace ohhhh pls just don't say it,

"Mohan!! dagaske ne Banafsha tana da ciki?

Surprisingly Alhj ya kalle sa kallon "irin wow,masha Allah.

,..shikuwa fargaba ne a fuskan sa

...hjy mahnoor jikin ta har bari yake tace ka amsa ni mohan
Isit true banafsha nada cikin ka?

..Hankali tashe ya dago suka hada ido bai iya cewa komai ba

sosai kirjin sa ya buga musamman jin muryan ta na rawa cikin bacin rai...riko hannun ta zaiyi ta fauce a fusace
Yace....mum pls listen to me...pls don't over react,
dama zan miki bayani..

sai tassssssss ya ji saukan wani lafiyyyen mari a fuskan sa.

"shut up mohan.. Wani bayanin banza zakiyi min when uve already dishonour me?mohan are you mad,ina hankalin ka yake ne..ta fashe masa da kuka.

Abunda Nimrah take so ta gani kenan sai ta fice daga wajen a guje ta fashe da kuka..

Cikin daren ta fizgo motar tayi hanyar gidan jamila hauka ne kawai ya kunce mata muraran har cikin jinin ta cizon ta yake

Mahnooor What's all this wai meke faruwa ne,..?calm down mana relax
Alhj ya riko ta Yana fada
kuka take mai cin rai tana nuna su
..kasa controlling fushin ta tayi Musamman data ga hjy mamah ta jawo hannun mohan din tana duba fuskan sa hankali a tashe,...

Tace....."Alhj mohan fa ya raina ni,anjuya min kan da na yanzu sam bayajin magana ta,kasan daya zo gidan nan ma wani wajen daban yaje?..,duk sabida yanzun yana da wata uwar na daban data fini daraja a rayuwar sa...

Cikin dakewa hjy mamah ta juyo tace Ke mahnoor,ya ishekii haka,ki iye bakin ki,ai sai kifito fili kiga yamin meye akayi miki kike neman daga wa mutane hankali

daga cewa Banafsha na dauke da ciki shine zaki haura kan yaro da duka.
Meyayi miki?

Hawayen ta ta share a zafafe cikin basar da maganan hjy ta dube sa,..abun kunya ka riga da ka jawo min"ashe kenan zaka iya tsayawa kana kula yarinya as premature as ur little sis nusaiba? Mohan Meye abun daukawa ajikin Banafsha har da zakayi mata wani ciki..

...toh in ni uwar ka ce yau zaka san yanda zakayi da cikin nan dan ba za'ayi pre-term birth agidan nan ba..

"Mahnooor!!!!!! Alhj ya daka mata tsawa a tsorace taja baya tayi shiru

,tuni mohan ya zube kan gwiwar sa yace Please,
Mum am sorry dan Allah kar kice hakan,nayi miki alkwari xan kula da ita,dan Allah ki fahimce ni

Wani tsawar zata daka masa alhj ya ce mata ya isah haka baki da hankali ne?
A ina aka taba yin haka...

Cike da tsiwa Tace ka ta tambaye ta man itace take karkatar min da tunanin dana, ai da chan mohan ba haka yake ba,da nace kar ya tsallaka kara bazai tsallaka ba..bur whats happening now.

Cikin tsananin mamaki alhj ya bude baki yana kallon ta'cikin ransa yana cewa anya mahnoor ne wannan?sosai Yaji ransa ya baci

"Zai yi magana hjy mamah ta daga masa hannu,wani irin daure fuska tayi wanda bata taba yin irin sa ba ta iso gaban su duka,..

Tace ehhh lallai kam mahnoor
,dama na dade ina jiran wannan ranar,ina dai kin fitar da abunda ke ranki?To bari ki karaji,dake da mijin naki da mohan din duk ina da cikakken iko da ku,da kin ki da kin so cikin Banafsha haifaffe Ne

 "pre term or not zamu raya shi,To Ke Ina ruwan ki? dake ko babu ke ni saddika zan raine dan mohan ya girma kisha kunya.....

Ai ni bazaki bani mamaki ba sabida da chan ma bakin san zafin mohan ba ni da kike cewa na juya masa kai akan ki aje a haka na amince

,ai uwar da ta san darajar farin cikin danta murna take
Idan tayi jika..

Duba da yadda muke fama ma gidan nan mohan ma kadai auren sa kusan shekara shida ne da wata macen amma babu haihuwa"

Juyowa tayi ta riko hannun mohan wanda tsanainin tashin hankali ya byyana a fuskan sa

Dakewa hjy mamah ta sake yi ta kalle alhaji dake tsaye ranshi na kuna...

tace turaki
Nayi maka rantsuwa da Allah kwarzani ko tarin habaici ya taba cikin dake jikin surkuwar ka sai na ga karshen albarkan ku kai da matar ka...

Mohan ajikin dana ya fito,
haihuwar sa kawai kikayi in kin mance ma Na tuno miki,hannun ki ya sake taba shi akan maganan cikin nan Allah ya isa ban yafe miki ba.

Ai ba zina yayi ya samo dan ba,ke kuma bazaki daura mana jahilci da ra'ayin yahudanci Ba,kinyi kadan kin kasa.

Sabida haka Wannan magana ma na kashe shi

"kai mohan yanzun kaje ka dauke matar ka ku shirya maza kuyi gidan ku inyaso kwa kwana acan

Mohan Jin wayannan maganganun yasa Jikin sa yayi matukar mutuwa

Hjy mama tace...nace ka wuce ka bani wuri ko?
Shasha sha saura naji kaima ka biye mata.

Alhj ne ya gyada masa kai alaman yayi hakan ba musu yayi sauri ya fice ya koma sama ya shiga hado musu kayan su suka bar gidan.

Ita kanta Banafsha bata san meyeke faruwa ba kuma bata ga alaman komai daga gare shi ba.

Hjy mahnoor zubewa tayi tana kuka wajen.

Alhj tsaban baiji dadin abun ba baiko kulata ba yabi bayan hjy mamah.

Itama haka ta bore mishi tana mai jaddada masa cewa
In har yana son kwanciyar hankali to yayi kokari ya dawo da mahnoor hankalin ta tun wuri kafin ta dau mummunan mataki akan su duka.....
@surayyahms#SURAYYAHMS
Things are tite ayi Hakuri Dani cikin kwanakin nan🙏

🍒🌺AJALIN SO🍒🌺

WATTPAD SURAYYAHMS

43.... the Hitch

Washe gari da safe A gidan jamila

Zaune suke su uku akan Dinning table mijin ta na mata magana amma hankalin ta nakan wayar ta tana latsawa"

...A jiya cikin dare Tunda Nimrah tazo gidan Ya rasa gane kanta

,shima xaiyi nisan tafiya ne amma ahakan ma sama sama take amsa shi wani bin ma ba daga abunda yace ba.

'daya gaji tsaki ya ja ya fice bata lura ba sai da kanwar ta hanifa ta ture plate din abincin itama cikin rashin jin dadin halin nata zata bar wajen.

"tace Ke hanifa,..wai har kin koshi?bata amsa ba taja tsaki itama

Ajiye wayar tayi son Sai a yanzun ta fahimce ta Bayan ta dago kai babu mijin nata a wajen,

sai ta dafe kai tace Ohhh ashe har ya fita ne....,Toh hanifa why don't you stop him bai Ma kira min doc din ba Ai

"cikin rashin kulawa hanifa tace Ai yayi kyau"
Ba kin samu aikin da yafi miki auren ki ba? Uwar ki nimrah tana gidan nan ai babu wanda zaki kula ko..

"Hey hey stop there hanifa ya haka ne kam,. wai kina ganin condition din data zo last night and yet u complaining Ban kula miji ba?

Nimrah was hyperactive fa?sai da aka mata allura tayi bacci.

"CikiN rashin kulawa hanifa tace Ohooo hmmm Uhmmm wai nikam hauka take ne?Ai inaji tana wani hargowa tana miki fashe fashe kawai bazan iya bata time dina na fito domin ta bane...

So Why dont you call her husband ko bata da dangi ne sai ke?

"ajiyan zuciya jamila tayi Agajiye tace,i dnt know.. jiya da daren Dai I tried calling Mohan da hjy mahnoor" amma duka is off
,sannan na kira hasina ta kashe min waya i was soo angry.

Wani kallon tara saura hanifan ke mata bata ce uffan ba ...

Ta cigaba Da maganan ta ...

"Hanifa this is serious,... a gaskiya ina ga wani mummunan abu ya faru da nimra jiya bayan rabuwar mu."

"zama hanifa tayi tace 'Hmmm to Ni ina ruwa na,chan ta matse muku,ni ke nake jiwa jamila yanzu bagashi akan hidimar ta kin yi banza da mijin ki ba?,Nimrah ce fa yo me xai sameta kuwa dayafi karfin atrocities dake kanta?.ni Ko ajiki na dan bata bani tausayi.

Jinjina ki jamila tayi "tace Hmm Eh kam Ai kuna da aiki keda hasina...,to gwara ita ma hasina nasan halin ta ne rashin mutunci,
amma Ke sam bana gane tsanan da kika daura ma kanki akan nimrah"

"Hankali Kwance hanifa Tace "ai bazaki gane ba Kekam,..
Nimrah is a wicked murderer jamila,You knew how she killed my friend aysha,dan
Mohan ya iya yafewa yana zama da ita matsayin matar sa nikam bazan yafe ba,i hate her
Gaskiyan lamarin kenan

"....Hah Dama nasani its alwys about ayshan A dead person,
cmon what's wrong with you ne hanifa.

Hanifa Hade rai tayi tace Nothing
...babu komai kije kiyi abunda ke gaban ki amma dai ni bazan taimaka miki da komai ba muddin akan wannan matar ce'.....
Kaiwa nan taja Pillown kujeran tayi Kwanciyar ta Basar...

Cikin haka sai ga mai aiki ta fito,.
..Jamila tace ya akayi?...taci abincin kuwa
Girgiza kai kawai mai aiki tayo,daga nan
Haurawa sama jamila tayi ta barsu anan...

Daga gidan alhj mu'amar tsaye Mohan yake A kofar dakin mahaifiyar shin yana wondering ina zata shiga da sassafen nan.

dankuwa ya duba ko ina agidan baiji ko motsin ta ba,

Where could mum be?agogon sa ya dada dubawa fuskan sa cike da fargaba da damuwa yaga its just 7am,...

Juyowar shi suka hade ido,hjy mamah ne tsaye alaman daga kitchen ta fito...

"Dan dauke kansa yayi daga nata Yace ina kwana,...?

Lpya ta amsa tana karasowa kusa dashi?.inche dai komai lpya yana ganka anan da sassafe.

Dan sosa kai yayi Yace dama mum nake nema ko kin ganta?Yadda yayi maganan jiki a muce sai ya Dan bata tausayi Cikin ranta

,.Tasan Baya jin dadi aransa, shikan sa in akace mahaifiyar sa zata nuna wani abu sabanin farin cikin Game da albarkan Da ubangiji ya azurta Dashi Da bazai yarda ba,.

Abun ya matukar damun sa Ko bacci baiyi ba

,...ajiyan ma Dan ya lura da yadda Banafshan ke kallon sa ne da suka tare gado zasuyi bacci Ya sausauta,... da alamun cewa
tasan yana cikin rashin walwalan
,amma da shike bata san meye ya faru bayan tafiyar ta ba sai ta biye masa akan babu komai din Da yace

"Hjya cikin son tayi sparking din Mood dinsa tace wai kuka kake yi ne Dan bakaga mahaifiyar kan ba?...Oh ni yau naga ikon Allah
Toh kwantar da hankalin ka Mahaifiyar ka yanzu fitar ta anan..,ai tazo da safen nan munyi magana Komai ya wuce,"

"batare da ya kalle ta ba ya Dan runtse idon sa ya Kuma budewa
...Wani kwalalan sanyi yaji aransa Na gudana bakinsa yana mai furta alhamdulillah Har cikin zuci..

"Yace to gashi dai na duba bata nan'
Kuma dad ma ya fita.
Hjy Batace masa komai ba don daga nan gefe akwai triangular couch Zama hjy tayi tukunna sannan tace'...
Its ok,maybe ta fita ne Zauna ina son magana da kai..

Zaman yayi babu musu

Kallo ta bishi da shi tana ganin yadda ya Sauke ajiyan zuciya may nauyi...

Tace a gaskiya Abun da ya faru jiya baiyi kyau ba sam,Mohan kar kaga nayi ma mahaifiyar ka

hakan agaban ka Kaima dauka ko bana mutunta kimar ta awajen ka Ne.

"Nasan hankalin ka bazai kwanta ba,yanzun Ma ai biyo takayi ko?

Yayi Dan gyaran murya Yace,eh toh Hjy Ai bance kinyi laifin komai ba amma bana son wannan fushi nata Ne...,Ni dama hakuri nazo na bata ko dama bazata yafe ni akan lokaci ba dai bana son hakan ya shafe Banafsha...murya kasa kasa ya karashe last words dinsa.

"Sosai hjya taji dadin wannan kalamin nasa Itama acikin ranta bata so ace Banafsha tasan meya Faru Ajiyan.
Gashi dama Da safen har tayi ma hjy Mhnoor
Kashe di akan haka..

Tace to ai mahnoor tazo da safe ta bani hakuri....i think everything is alright now...
kasan mu mata abu kadan wani lokaci sai mu maida shi babba.

Yace haka ne Am glad an fahimci juna. But still zan bata hakurin dai
Nasan jiya da bacin rai na ta kwana.

Tace haka ne,kar ka kuma daga hankalin ka kaima Akan haka..

Kamar yadda kace,..toh babu ruwan Banafsha da jin wannan magana Allah Dai ya sauke ta lpya kawai,kaima Allah yayi maka albarka.

Ameen yace yana jin saukin nauyin dake zuciyar sa...
Mikewa yayi yana gyara zaman all black suit dinsa
Wansa yayu masa das das

...yace ni zan tafi..
Anan sukayi sallama ya fice.

fannin hjya mahnoor kuwa tunda ta bar site din su hjy mamah da safen ba inda ta nufa sai gidan mahaifiyar ta hjya zaynabah..

"agaban ta ta zauna,cikin jimami take cewa".....

Ummah Rabo na da naga bacin ran alhj irin na daren jiya yau akallah mun kai shekeru ashirin'.
Kenan ni bani da iko da gida na har da na ma ta kwace min tarbiyan sa?

Ummah am sure mohan baida laifi wallhh saka shi sukayi ya ma yarinyar Chan ciki dan kawaye na suyi min dariya.

"Hankali kwance hjy zainaba tayi murmushin manya"
...Tace toh menene mafita? Kinga zuwan ki gidan nan sam mahaifin ki baya so,kar ki manta wannan auren naki shine darajar mu a duniya baki daya.

Umma ni dai gaskiya nagaji da abunda take min..,shikenan sai na kyale ta tana controling kowa da komai
..Kinga bacin ran da miji na ya nuna min kuwa ni kaina bason raina na bata hakurin nan ba.'

"Hmmm mahnoor kenan,..har yanzu dai baki girma ba
Ni nan nasan wacece sadika Yoh ina ke ina fito na fito da ita,?ni bawai ina ce miki bana supporting dinki bane'
Amma na lura wayannan matan r just looking for a slightest way to replace you a rayuwan muamar,
so suke ya kara aure ko ma yasake ki suci arzikin suka dai...,

"..Tabbb ummah?Ai kuwa hakan bazaiyu ba....

Hjya zaynab tace....Zaiyu mana mahnoor ?uwar shi ce fa...da a son samu ace kece daya masa tamkar asiyan fir'auna a ma sarauta,sai dai hausawa sunce fadan da yafi karfin ka sai ka maida shi wasa.

Mahnoor,ki bar su ahakan ke ki ji da danki mohan,
Mohan dama baya jin magana.
bokon nan ya taurara masa rai

rayuwar turawan nan gareshi,yo kina uwar tasa zaki ce kar yayi kuma yayi har ya boye miki?shi gashi ya mallake gohon kansa ko?

",..yanzu dai ya rage naki ki koya masa hankali,so nake ki cire son uwa kima sa hukuncin da nan gaba bazai sake kuskure irin wannan ba'

ina laifin yayi ma yar ministan nan ciki kema ai xaki amfana muma kuma anan zamu amfana..lokacin campaign yayi ya kamata muma mu zamto daya daga cikin ahalin
Siyasan wannan kasa.

Amma wanga karamar yarinya ba yar kowa ba..'goguwar rabon cin arzikin alhj ya kawo ta...wannan jikar tako dake cikin tan mi xaki amfana da shi?..
Yanzu rayuwa ta canza daka yi rainon asara gwara ba ayi cikin ba

A matsayin ki?Ai Jikar ki ya kamata ace nan gaba shine abun alfaharin mu...

Amma wanga y'a da yayi wa ciki kenan dame zamuyi mata guda?mu zamu kai ko mu za akawo mana raddi.

Tagumi hjy mahnoor tayi tana jin wayannan bayanan Batce komai ba...

..hmmm uhum toh ba'a dai kin jini fa..ai xaki rike jikan naki ko?

..,amma naso Dai ace mohan yana da tunani mai zurfi...

Ummah ai gani yake Yana da shi din,shi sam baya hangen nesa.

"Haka ne kAm,ni kaina Nasan mohan yana da arziki amma idan siyasan nan ta shiga masa ai ma dada hutawa ko?..sai kiji wata rana ma ance jika na mohan ya zamto shugabann kasa Amma shi so ya ke ya shashantar da auren na nasa da yar minister,ya nanike wajen bin ra'ayin sadika...
Allah dai ya kyauta

A take Hjy mahnoor ta dago tace ameen ummmah,
wannan ai duk ya wuce,..Nidai zan dauki mataki..dan gaskiya bazan yarda ba.

Hjy zaynaba da wuri ta tsare ta Tace toh,kar dai naji tsakanin ki da mijin ki an sami matsala..
Kibi su yadda suke suke so din,Allah ya sauke yarinyar lpya
Mohan dai shine miki abun duba
Maza Tashi kije gida kiyii nazari.

Nan Ta mike tace toh ummah su kayi sallama.

Bangaren Nimrah kuwa,zaune take tana kuka Daga bakin gadon jamila...

cikin tsananin damuwa jamila tace ..."Dan Allah ki fada min meya faru..i can't get everything Straight..wai shin
Kunyi fada da mohan din ne?

Bakin ta har na rawa....tace "ah'a
,bamuyi ba jamila mohan Dai ya cuce ni,.. Ya kuma tozarta ni...i won't eva forgive him'...he just lied and deceive me...cikin matsanancin kuka take fada.

"Karyan me ya miki?what Really happen.. .jamila tafada out of curiosity

Nimrah Kukan ta cigaba da yi bata ce komai ba sai da sukaji an bude kofa,

Gasu nan anan wajen hanifa ta fada
...ta ja gefe itama ta tsaya.

Hasena ce ta Shigo Kwas kwasa kamar sarauniya all on fleek sanye Da Wata matsatten office officials dress dark Red da baki,
"Zama hasinan tayi Daga gefen ta, ta dafe kafadar ta Cikin mamakin ganin yadda ta dawo Pale Alaman taci kuka Sosai, tace nini?...who deceived who?Naji kina cewa an cuce ki...meya faru ne

...Cije baki nimrah tayi wani hawayen na tahowa Tana tarewa Da hannu...,Komai ma ayanzu its actually paining her Don Har tana barin baki Tayi magana.

Tace can you Guys imagine.. mohan Ne fa wai yayi ma yarinyar nan ciki

And they were hiding it sai jiya asirin su ya tonu....i Just cudnt take it...sai Ta riko hannun jamila ta sake nishi mai zafi
.
A garin yaya?Out of tension hasina ta tambaya...

Cikin wata sabon kukan Nimrah Tace I dont know Ni bansan musu ba,mum Fa har ce masa tayi kar yana kwanciyar aure da ita and he kept fooling me all this while tht baya kula ta i tot tayi masa karama Ai...ohH mohan,He is bastard How cud he?"..i just don't know what to do ta cigaba da kukan Ranta a dagule

Galala dukan su suka tsaya suna binta da ido banda hanifa da already ta soma mata dariya Mi ban haushi Tana mamakin ta.

..yanzun kina nufin mohan wai yayi ma kishiyar ki ciki?...Wannan karamar yarinyar
Wani Shiru ne ya ratsa wajen

Kallon Kallon Jamila da hsinah suka yi ma juna zuciyoyin su cike da ajijiyan gurmi".

So,har Yayi mata ciki?Hmmm.
Nan Hasina Da jamila Suka fada atare Suka dan tafa Hannu Mockingly...

Wani kukan nimrah ta sake bata Ko amsa Su ba...

Jamila ce tayi saurin isowa gareta ta shiga rarrashin ta"Allah zai saka maki friend,gaskiya bai kyauta ba
. amma ko dai mohan bai cikin hankalin sa ne,.."kan kafadar jamila ta koma tana cewa Oho nasan DaI hankalin sa jamila wallhy dagske ne,

Nifa nasan da ban bar wajen ba ajiyan nan wallhy Da bazasu kwana lpya ba

Oh Zaki kashe su ko? Hanifa tayi mata tambayar cikin gatse.

..wani zazzafan harara ta Dago ta Bita da shi tace bazan dai kyale su ba mohan yayi kadan yaci amana Ta na barsa...
Ai yasani sarai darajan lady yakeci shida matar na sa Da Sai na....

Ke!!!nini pls stop there ...hasinah tafada cikin bacin rai mai tafe da annoyance

..wai yanzu akan wannan abun kike wannan haukar?tabb di jam..toh ina laifin sa guda anan..ThiS issue Is simple They are married and he got her pregnant... so what? Meye sabon abu aciki..

Itama hararan ta watsa mata cikin kuka tace'tun da baki ga komai aciki ba ni nan nagani kuma zan ci uban su duka
..tashi tayi kamar mahaukaciya zata fita jamila ta rirriko ta,tana cewa CaLm down

Daukw da siririm Harara Hanifa tace..."Battta Jamila
,batta taje mana...wargi ma ai waje ya samo
...ke dan ke dakikiyace sai mijin Naki ya tsaya jin wannan useless issure din?
I mean ure just just His wife ,ke din wacece da zaki gaya masa abunda xaiyi da kishiyar ki?

"rai abace Nimrahn tace,but He lies...

"so what? Hanifan ta daga mata murya Kamar zata buge ta...,ke sau nawa kike masa karya?Ai kedin shasha Sha ce,mutum da matar Har sai kuyi tunanin bazai rabeta ba?..

Tabe baki hasinah tayi tace Ohoo gaya mata dai hanifa..ni wallhy da nasan haka ne da banzo ba.

Kallon su duka Nimrah tayi irin oh haka ma zakuce min

..Wani kakkauran Tsaki taja ta fauce kanta a jikin jamila...

"Ba dauka ta kuke mahaukaciya ba,i will show you what i can do Ta wani fixge Xata fita...

irin dariyar rainin wayon nan hanifa ta sake,ayyuriiiri tayi gudan ta mai ban haushi
Ai inda rabon shan duka Allah ya bada hakuri baya magani,
kadan kika fara gani wallhy ,kedin banza acikin matar ma ke cusa kan naki ya wuce misali Wlhy ....mohan dai yayi miki nisa, Kinyi kisan Kan ma Kuma yasani amma Har yau baki mallake sa

Wani hargowa Nimrah tayi ta jefe ta da jakar ta cikin tsananin bacin rai tace sai naci ubanki hanifa...walllhy sai na gurje miki baki anan wajen.

Mohan is mine kuma sai nayi ajalin son duk wata mai son sa a doron kasa"
Nafada miki kenan

Hanifa bata fasa ba tace Ahayye ai a da kenan,...kike tashen ajalin son mohan.. yanzu kam Da kan mage ya waye Wllhy baki isa ba,gashi nan dai angama cika mana baki akan Kishiya Sai ga ciki hahaha
..,yadda kike yaudarar mutane haka aka yaudare ki..our wife,aysha's successor is pregnant....Allah ya sauke ta lpya Ameen.Kedai Aje dai arungumi bakin ciki Mune dai first...Gyara kwalin kata tayi tayi tsaki

Da kamar zata hakura amma daga bisani"da wani irin fushi ta Fusato ta sauke ma hanifa mari itama tabi ta rama A take

Fada ne ya tshi kurewa tsakanin su Su hasinah ne suka taro su

Nimrah Huci take har tana kyarma Hannun ta ta fauce "pls let me go,jamila wannan sister kin neman kiris dama take ta zazzage ni..
To ta Allah bata ki ba.munafuka..

Dariya hanifa tayi tace kije aji da bakin ciki dan wallhy hakkin innocent aysha will forever follow you and kill you Into slow death, ...painful death..Apostate of hell kawai

"Ohhh gosh you two Ya isa haka,hanifa ya isa,..

Nimrah pls calm down ..a Matukar hrxuke tace "no am leaving,hasis mu tafi...nan tayi gaba hasinah na binta abaya....

Meyasa hakan ne
Hanifa
 wai ma waye ya tsoma bakin ki cikin maganan nan Ne ma?
Gashi kin bata mata rai shikenan hankalin ki ya kwanta?

Hanifa tace Eh mana,taje cahn ta cigaba da haukar nata Allah ya sa ya sake ta ma kowa ya huta

"Hey enough,im being serious here hanifa dan Allah ki dena wannan abun naki da Nimrah,
iF i loose her Kinga ai all my business depends on her connections...ko so kike ki jawo min fitina da asarah Ne?

Look u have to apologize ooo dolE xaki bata hakuri

Dariya hanifa tayi tukum Sannan tace Uhum ok o..toh am sorry oo dan ita kam tasan ko na fada sai Dai na fatar baki...nidai bana kaunar ta kuma bazan so ta.

Anan kuma Cikin motar,.. hassina ce mai jansu tana kanunun magana itama ..
" Nimrah kina bani mamaki Kiga fa yadda kika kassara rayuwar ki akn namijin da baima sam kinayi ba

... its 9oclok in the morning kiduba ,wai shin ya ma san inda kika kwana bare yasan halin da kika shiga ciki Akansa?

Ai gaskiya hanifa tafadi...that ur mohan Is a beast..wai duk da ma sihirin naku da su mum
Kenan amma dai banga alaman yana kaunar ki ba,...
A hatsale Nimrah tace
Thats none of ur business hasinah,
Naga kowa gaya min magana yake son ransa sabida bakusan ya nake ji ba ko?

Mohan yaso ko kar yaso ni ce matar sa kuma Dan dolen sa sai ya so ni

cikin tsananin takaici hasinah ta tabe baki Daga bakin gate tana danna horn,...Ta furta
Allah ya kyauta dai,..
but im advising you to get back to your Senses walllhy wannan haukr taki bata da aji..Kamar ba mace ba

Nimrah Tsaki tayi ta bude motar daga bakin gate Din ta sauko tun kafin ma hasinah ta shigo,..

Tafiya rai abace ko juyi batayi b bare tace sai anjima.

"dariya haseenh tayi tace toh!Hmmm lallai fa,ran mata ya baci ,hm Indai akan namiji ne,to zaki ko kashe kanki kuwa nonsense taja motar ta ta tafi,

Da wani irin daure fuska ta Shigo gidan, dai dai banafsha tana saukowa Kenan itama zata nufi kitchen.

Da suka hade ido Tsaban huci saida Nimrah ta rike zuciyar ta dake neman tunzira ta tayi mummunan abu..

Banafsha ko ajikin ta tazo zata wuce kasan makoshi tace
"Ina kwana anty

Bata ko bari ta karaso ba da Wani Irin cahkumi tayi ma rigar baccin dake jikin ta ta dawo da ita baya tana mata kallon deban Albarka.

Tsoro ne ya so ya zo mata amma sai ta cije,itama ta kalle ta,...

Ke!!!wato har kin san maza ko?..gaki mai cikin shege Kin fito xaki min yawo agida na ko?..

"Nidai ciki na ba shege bane da uban sa

..nimrah in shock ta kalle bakin Banafsha daya furta magana a tsananin rawan murya.

Saketa tayi ta hade hannu,irin wow?..wato an san namiji har an fara amsa min magana

"Cikin masifa tace ina magana kina amsa min toh wata rana sai na gurji bakin ki..

Banafsha Shiru tayi mata Ta yunkura again
,zata wice ta daka mata Tsawa a firgice Sai da ta Ja ta tsaya...

Cikin dakewa da rashin son nuna halin data ke ciki boro boro' tace ke kiji ki kara ji na wannan lambar karuwan cin da ke jikin ki,kike kuma yawo min da shi agida kwanan sa sai ya kare...

Cikin murguda baki Banafsha tace ..Ohhh Ai bake kika min cikin ba,kuma wallhy sai na haife sa ...ni wallhy ki kyale ni...i want to go.. nan Taja gefe xata wuce nimrahn ta tsare ta again
Ki kace banii nayi miki ciki ba ke baki jin kunyar kanki,karama dake kina fadan hakan?
What do you know about men bare kuma miji na mohan,"
...Which im sure ke kika kai masa kanki marar tarbiya kawai ta dungure ta.. for that sai naci ubanki agidan nan..so mean and angry ta fada

Wannan abu ya sosa ma Banafsha rai amma hakan ta ki ta sake hawayen dake cicciyo ta a ido,wani irin
Tsaki ne ya kufce mata...a harzuke nimrah ta dago hannu zata maka mata tayi sauri ta ture hannin nata ta koma gefe.

Hawayen daya kufce matan tayi saurin sharewa ta daure fuskan ta Sosai,

"mamaki nimrah tasha datayi hakan,amma still tace ai da kin tsaya na fasa bakin,..."

Bari kiji.. Don kinga kina da ciki dosnt mean that kin samu bakin da zaki raina ni Im not your mate Banafsha

besides,kinsan baki kai nayi kishin komai dake ba,da cahn dai ina tausaya miki amma tunda kin baude ma kanki kin saya fitina yau zan nuna miki matsayin ki..

Banafsha na shiru abun ta wanda gakan ke dada kona ma nimrah zuciyah.

"tace shin kinsan miji dai nawa ne ko?..kallon kasan ido banafsha ta bita da shi ta kau da kai

Ba sassauci tazo gaban Banafshan tana buga Kirji,..ai yanzu kinsan komai tunda jaraban ki ya sa kin samo abun da kike so..."are you not tired of being a slave? I bet duk randa kika gane jikin

naki ma banza Ne awajen sa zaki raina kanki..

Nimrah Juyi tayi gaban ta ce wai Ina hadin waina da kashin shanu?

..mohan worships my body,..he begs to have sex with me,..cikin wani dan iskan gurnani tayi dariyah mai cin rai mai ban haushi...
Kamar bata cikin hankalin ta tayi describing yadda suke juya juna musamman ma ta fannin sa.....

Shiru Banafsha tayi tana jin ta sosai...

Nimrah data Samo hanyar rage fushin nata Cikin son ta kular da ita tace kekam ai rokan sa kikayi,yo
Wani jin dadi M zakuyi? He dosnt love you and he won't,ke dai baiwace har yanzu.

"rayin Banafsha ya baci amma ta yi kokarin saka shi acikin ranta
Tace anty,why are you telling me all this ..

Da wuri ta katse ta tace
"sabida ki kama kanki,kina da cikin mohan ne amma baki da mohan a rayuwar ki...baki gani ba 6yrs muna tare he's just enjoying my flowing juice, basai kuma nayi ciki dan na same kansa ba,kinsan ni ba sarar ki bace ko And i will neva be...

Banafsha tace hmmm'....indai haka ne zancen naki toh ashe ma nafiki awajen sa..anty nifa ba baiwar kow MA bane and i will Neva be

Just the way he made love to you nima hakan yake yi min...
Itama rufe idanun ta tayi ta bushe ido tayi mata describing yadda suke juya juna..

.nata da shike na dauke da yarinta sai ya kasance kalmomin tan ya kazanta har kalar zufan da mohan yake yi sai da ta bayyana mata"

Idanun Nimrah saida suka taro ruwa cikim ranta sai sa ta tambaye kanta meya kaita buga wannan game din? A Tunanin yadda taaan Banafsha as weak and vulnerable in ta gaya mata maganganu haka zata cusa mata ra'ayi da bakin cikin daukar cikin datayi,

Amma yau sai taga kamar ba Banafshan ta iskance fiye da yadda take zato
...she neva tot that yarinyar zata iya amsa magana akan cikin dake jikin ta bare sex din da sukeyi da mohan

Ita kawai tayi hakan ne domin ta harhado karyan da zai bata daman kau da cikin Banafsha ta cikin wani sigar makirci da lumana da kuma hassasa mummanan gaba a tsakanin su akan haka.

But Whith the way Banafsha reacted yau wani karin bakin cikin tajiyo ma ranta cikin ranta tace ","wai Dama mohan hakan yake yi ajikin yarinyar nan? Ko karya ta yanko min kamar yadda na yanko mata nima..
"Oh my God im dead,ko dai nima zanyi cikin nan ne,anya yarinyar na bata bude idon yati over ba?...ohh lord. What will i do now,mezan gaya mata taji haushi ta cire cikin nan da hanun ta...i have to think of something... i have to thinnnnk tafada cikim zaucewa maganan har ya fito fili bata sani..

Wani sabon salon Tsakin cikin wuya Banafsha tayi zata wuce tace

"Ke !!!? Ta dago cikin wani tsawa tana kallon ta..

Sallamar sa ya katse su dukan su sai sukayii shiru,....

Wani mugun kallo nimrah take binshi da shi Kamar wacce zata kashe shi
...abubuwa dayawa tana tunowa amma tsaban kishi abunda Banafsha tace mata yanzun take kallon sa da shi...harji take numfashin ta na tafiya sama sama..

Ya kalle su duka baice komai ba sai sa cikin Ransa yace what's going on here...

Babu Wani jira Banafshan ta kwaryo kwana zuwa inda yake daga tsaye zata tare sa da welcome shagwaban nata da ta saba Masa

..tana daga kafa sau biyu
A hatsale Nimrah tace ke!!!come back here bangama da ke ba..

Banafsha ko Bata tsaya ba saida ta isa jikin sa a lokacin shima ya hade rai yana tambayar nimran meya faru take ihu a gidan..

Wani larnewa Banafshan tayi akan kirjin sa ta kankamo sa...
,kawai sai sukaji sautin kuka...

Abun ya fara fin karfin dauriyar nimrah a lokacin wani karfi take ji Don a shirye take ta yi musu wani mummunan action

Shi kansa baisan
Sanda ya shiga halin zautuwa ba ayayin da yake shishigewa cikin face dinta yana tambayar ta Meya same ta

Asalin ita ba ma kukan take ba danko hawayen ta da ta taro dazun ganin sa ya sa ta komar dasu,burin ta bai wuCe ta nuna ma Nimrah ita ma mace ce agabn sa ba,

Dada boye fuskan take Arms dinsa,da shike kukan makirci ne kuwa sai yafi fitar da zakin sautin

sa Sosai...dada kankame Sa take tana shigewa jikin sa...cikin sHeshekr karya Ta make kafada cikin salo tace yaya wai da gaske ciki na cikin shege ne?

Rungumota yayi batare Da yasan yayi hakan ba yace kul na sake jin haka abakin ki?Are u insane..

Cikin wani
Dan iskan fitinnanan shagwaba ma dauke Da shauki Mai birkitarwa tace ai bani nace ba Kawai ni ka fada Min,..ta dan shiga bubbuga kafa akasa

Yace Toh Wayace miki gaya min naji
,
Batace Komai ba ,cikin yauqi da saibi Take matse idanun ta,..Dan zamewa tayi
Kadan Ajikin san ta yadda Nimrahn ce kawai xata ga real fake Cryng face din ta,
sannan ta ya mutsa fuska ta nuna mishi ita da hannu ta A sakalce tana dada sa sautin kukan karyan suna kallon juna da Nimrah..
Follow#SURAYYAHMS @surayyahms

🌺🍒AJALIN SO🌺🍒

WATTPAD SURAYYAHMS

44-the unforseen

Wani irin Kallon mamaki da takaici nimrah take Yi ma Banafshan ta rasa me ma za tayi musu dukan sun don ta huce..

Zuciyan ta ne kw mata zafi..tasan Inta tsaya nan gaba dayan su babu Wanda zaiji dadin abunda zai biyo baya

,gashi sam bata so ta fara bata rawan ta da tsalle agaban su duka.

Maganan zuci take,fuskan ta a murtuke kamar zata fashe

"I really want to deal with her,sai naga karshen numfashin ki A duniya."and
As for you mohan,ta galla masa harara

U will surely regret this...

A fusace ta juya kamar wacce aka danna Mata remote control Ta nufi Hanyar daki

..yana mata magana bata ma jin meya ke cewa
..
a Matukar Hatsale ta Banke door din ta shiga site din ta,daga nan ma tanajin kiransa amma bata ko ansa ba bare ta tsaya Wani tunani

Ganin bazata kula sa Din ba sai shima ya baSar

"juyowa yayi ya kalle banafshan
...,Dan ko lura da busashun idanun ta baiyi ba, ganin reactions din Nimrahn sai yake jin tausayin ta Aransa..

But i will not allow this'no one will hurt you"...ya fada cikin ransa of strict assurerity.

"Stay right here ko daki zaki je ne?..,ya tanbaye ta yana janye ta ajikin sa .ita kuwa gani take kamar zai bi bayan nimrahn ne

,...lumui tayi da idanu kamar wance bata jin dadi ta gyada masa kai tare da cewa dama kitchen zanje Kawai,
Ko zaka ci abinci?

Gefen fuskan ta ya shafa kadan yace Not now

Shiru tayi cikin wani sabon salon sanyin jiki da ta ara mai dauke da shagwaba.

OK go on,ya fada Mata sannan ya Fara haurawa Sama..

...,Kamar ta juya ta tafi amma Sai taji takasa Motsi,..
yi take kamar wacce bata da laka,nan ta dago ta kalle Bayan sa Yana Haurawan Baima juyo ba.

For the first taji wani abu daban azuciyan ta
"..ina ma ace yaya mohan miji na ne ni kadai...

Tsaki ne ya kufce mata haka kawai ta soma tuno da maganganun nimrah na dazun.

Karshe Fasa shiga kitchen din tayi ta koma dakin ta,..
daga bakin gadon ta ta Nema waje ta zauna cikin tunanin rayuwar auren ta da mohan

nothing reasonable came cikin kwakwalwar ta
, gaba daya sai ta ji ta kasa tabuka komai cos mind dinta is already distracted da bin nimrah sama dayayi

tunanin ta hala yanzun yana wajen Nimrahn ne yana rarrashin ta.

Wani hade fuska tayi ta kife kanta ajikin pillow bai mata ba ta hauro sama ta kwanta da baya idanun ta na kallon sama

..."She actually hate to think of that..
...,gani take ko wace mace zatayi masa irin shagwaba da kirsan da takeyi ajikin sa...

Ko Kadan Bata so ta sa kishin yadda take ji ajikin sa In suna tare..gani take kamar bazata iya Cigaba da daurewa ba.

Tunanin irin Hakan Sai ya jefa ta wani hali,a duk sanda ta tuno yanayin wargajijin jikin nimrah ga nonowa radada har sun zubo Kirjin ta Sun cika Matured and riped.

Sai ta kuma kalli nata dan dai dai wani fargaba Da kishi ne ke rufe ta,.
.
..,amma still yanzun ji take aranta kamar zata iya ragin ta da wani abu awajen sa

Kanta ta tsinta Dayin murmushi
..shafo cikinta ta shigayi,tana tuno da fuskan sa..

Cikin wani sassanyar lumshe ido ta shiga zugo qamshin sa
...The wonderful feeling of bliss
...,shaukin sa take ji har cikin ranta,tsumayin sa yanabi ta cikin jinin jikin ta
..She want to kiss him,deep,erotic,dirty..And passionately'..,hakan kawai take ji yanzun aranta.

Take ta fara imagining komai akan ta,she wished and wished That zai shigo,amma shiru sai juyi take from end to end tana dada xurfafa acikin yanayin

Jin yadda abun ya tada dukan hankalin ta yasa tayi juyi ta kankame pillow tare da matse sauyayyun idanun ta ciki a hankali....

...slowly take sauke numfashi
,..har bacci ya dauke ta.

Bangaren Nimrah kuwa,tajira taga ko zai biyo ta taji shiru,shikam ma ashe dakin sa ya shiga ya cigaba da abunda ke gabar sa.....she was not only angry but highly provocked,... yau na daya daga cikim ranakun da suka kafa tarihi a rayuwar ta,gani take kamar an buge ta ne kuma aka hana ta kuka.

controling her temper is one of her greatest weakness and challenge.

..yau tasan badon lady zineta ba da Banafsha ta tsufa a rami.

....she realy want to kill her don hakan ne kawai kwalwalta ke iya kayyadewa a matsayin hukunci ko samun sauki

Nimrah da kyar ta samo nitsuwa
,daga nan Wanka ta fada ta shirya kanta izuwa wata simple English wax wanda ya dauke ta ras ,dinkin A shape ce daya sha pattern designs
..wanda ya dada nuna alaman fadawan fuskan ta

Its after 12m na rana har yanzu mohan bai shigo ba. "hmmmm ta sake tare da kada kai...drawer ta ta jawo ta balle maganin ta..
,batasan hannun ta na rawa ba har sai da ta je dago bottle Water ya subuce ya fadi kasa.

A dungure ta daba duwawun ta akan gadon tana wani numfashi.
Lumshe ido tayi tana neman Makan ta sauki

Jefo maganin tayi abakin ta ta hade shi batare da ruwan ba,..

Ba abun da ya ke daga mata sense yanzu kamar yadda take ganin bazata iya zuwa wajen lady a wannan yanayin neman mafita ba

,tasan siyasa ya kunno kai lady bazata ma saurare ta akan maganan nan ba..

Banafsha tamkar wani babban gurbin alkwari ne tsakanin ta da alhj muma'ar...for any reason tasan bazata iya kashe ta ba anytime soon ba.

Rayo wayannan tots din yasa ta sulale kasa"..this girl is a Curse to my life..ko da shiike ba laifin ta bane mohan ne,shiya jawo min wannan tsiyar daya rabe jikin ta'how cud he?wai me guda daya na rasa ajiki na..maybe he just want to humiliate me..kuma bai isa ba

wani drawer ta bude a haukace ta fito da gazal,dan tsinken cikin tafitar ta kira sunan sa sau uku,sannan ta goga a idanun ta ta nufi dakin sa.

so unfurtnate ta buga kofar taji shiru,..

murdawan da zatayi sai taga ashe ma baya gidan, Damn it ta furta cikin inert disappointment

dakin ta ta koma ta cigaba da tunanin yadda zata shawo kan al'marin

shikuwa mohan ashe tunda secrtaryn hjy mahnoor ya gaya masa maman sa tana office,sai ya dada shiryawa kawai ya fito

Kafin ya fitan ma lekowa yayi yaga Banafshan na barci,

.bai shigo ciki ba amma sai da ya kulle ta da keys din shi ta waje
...,kafin ya kara da gaba.

Daga offishin hjy mahnoor
"yayi kusan awa guda a tsaye bata ce masa ya shigo ba an ajiye shi awaje abunda ba a taba masa ba

Gashi models da sauran zaratan matar dake aikin designs masu zagaya..,super fashionistas,ana ta kallon sa kowa da irin salon shiashigi da iyeyin da suke masa...

"...he got pissed..
Da a wani wajen ne wani ya aje shi hakan da zaice pure wulakanci ne...

Agogon sa ya dada dubawa yana wondering

shi sam Aransa bai kawo' purnishing dinsa take yi ba,

sai Chan da yaga zuwan wasu client da aka masa karyan dasu ne take meeting Din tun zuwar sa Kafin ya taso

rai abace ya wuce kai tsaye zai shiga offisin sectaryn yayu saurin shan gaban sa Yace"sir please..wait..hjya tace kar na bar ka Ka shigo sai ta bada izini...
Strict oder Sir ..

Wani hade rai mohan Yayi...irin nida offishin mahaifiya ta ace min na jira? baima jira ya karasa Maganan ba ya bangaje shi ya shiga.
Yana daga ido
"He cudnt believe his eyes yadda yagan ta zaune cikin nitsuwa sanye da wani kasaitaciyar shiga ta alfarma

fuskan ta cike da kwanciyar
Hankali yake tana rubuce rubucen ta tamkar wata first ladyn kasa,...

She's alone shine mum ta ajiye ni fiye da awa awaje harda samin restrictions?

Abun ya bashi mamaki matuka.

duk dama sectary ya biyo bayan sa da korafi amma
Ko daga ido takalle su batayi ba..

Just Get out

.. yafada ma sectaryn rai abace,

Shikuwa sec kallon ta yake yana Kuma jin shakkar idanun mohan Ya rasa yadda zaiyi.

yana Kuwa juyI zai fita cikin muryan ta na kasaita tace ahmad,wai meye na fada maka ne?...dint i ask you not to let anyone in?

Mohan Ya juyo yace MUM?Cikin mamaki yana kallon ta,amma wani hade rai tayi
kamar bata san dashi ba.

Nan Ta cigaba da azalzalan sectayn ta Da masifa marasa Kama Kai...

SHi Sai yanzu duK ya fahimce ta..Fushi Take Yi Da shi

Mohan Kansa ya sauke kasa zuciyan sa na hana shi yarda da manufan reaction din mum din san.

Jiki na rawa ahmd Yace "Sir...sir.. please can you,..pls wait outside..

Ya dago yace mum i just want to see you..pls let me explain Things...mumy pls..

Yadda ya fada in slow shock Da fuskan damuwa yasa taji wani iri aranta Sai ta dan kalle sa..

Sai dai Batace komai ba haka ta dada bata rai
kasan makoshi tace masa Kaje kawai im busy..'

Sai Ta maida kanta Ka rubutun dake gaba tan Cikin Rashin kulawa ta furta
...As you can see.

Mohan Bai iya cewa komai Ba Kallon ta yake duk jikin sa a muce

'..Mamakin yadda ta murtike fuska tayi Masa maganan yayi sannan ya fice a sadade,.."

Sai da yafita ta dago tace ma ahmad
Duba min shi ya tafi ko?...

Lekowa ahmad yayi ya gansa zaune akan waiting chair ya dan dafe kansa.

Ah'a hajya bai tafi ba,..

Taji dadin hakan amma sai ta rasa meyesa bazata iya hakuri ta yafe shi ba,she loves mohan so much Wuce sanin kowa..

Amma bata so ta yi wasa tarbiyan sa ya kufce mata hannu.

I just want him to know im his mother,nan gaba magana Na zaiji ba Na wasu ba.

Haka yaci zama ga tarin apoitnments agaban sa na ranar baki daya Amma baije ba,

After like 3hrs sai ga ta tafito,..sosai ta tausaya masa musamman yadda ya hade kai da rest wall din kujera yana kan jira, tasan baiya jin dadi aransa.

Is this how much he loves me?
Ko dai dan bai taba min laifi Nayi fushi da shi bane?

Wuce shi tazo zatayi cikin wannan tunani amma babu alaman ta ma sanda Shi awajen Akan fuskan ta

Shikuwa Kamar zai mata kuka ya mike ya taho
,yace mum pls we need to talk,
hankali na bazai kwanta ba muddin kina fushi dani.

Kallo daya tamasa ta dauke kanta Kamar bazata amsa ba Cahn tace ...

Bani da lokaci say it now ina jin ka.
Kudu da arewa ya duba yaga agaban mutane fa suke,..yace mum ko zamu koma office...

Wani mugun harara ta balla masa har Bai san sanda ya sauke kansa kasa ba

...cikin dakewa tace,idan bazaka fada anan ba,you can excuse me.

am going out..

Tsaban takaicin dake cin shi bai iya wani kwakwarn magana ba yace Matato shikenan mum adawo lpya...

Tana jira taga yayi zuciya ya fice Afusace amma sai yaja ya tsaya har sanda ta fita shima ya fito ya shiga motar sa.

Whats wrong with mum?
...yanzu akan wannan silly issure ne har ta fara wulakan tani'ko dai dana na mata wani laifi ne na daban.?.
Abubuwa dayawa ya raya aransa

Tukin yake kamar ba zaiyi ba don Gaba daya idanun sa suka kada sukayi ja.

A duniya ya tsani abunda zai taba mishi ita
..kuma bayajin zai iya hutawa inhar bata sauko ta yafe shi ba.

Consultant office dinsa ya nufa,daga nan kuma Gida ya koma inda ya tarar da bakowa a tsakar Master Falon gidan

dakin sa ya nufa yana sauke gajiyyun ajiyan zuciya..wanka ya fada inda ya dafe bango shower da ya sake tana Zubo ruwa tana dokan bayan sa.

Ya dade anan Bai dago ba sai da yaji dai dai aransa ...

towel blue mai laushi ne a hannun sa yana goge faffadn kirjin sa Izuwa kunnen Sa

Dan kadan ya murza hand and feet cream,sai wani firming face chap daya goga ma radiant face din sa mai sanyi da qamshi mai shiga jiki,

Duk dama baijin fitowa wajen ko wanne daga cikin matar nasa but Yasan dole ne ya dubo Banafsha yaga lpyar ta
dan haka turaren jasmine din Data ke so ya dauko ya goga ma wani exclusive shot and eric vest dinsa

wato irin guntun wandon nan ne mai kama da beach shot matured yellow eric vest din kuma baki tana da kauri sannan ta kama siffar jikin sa damas.

Baici komai ba,ganin time din ishai yasako kai sai ya sanya jallabiyar sa akai ya nufi masallaci

Anan ne ma daya dawo zai koma dakin sa yaga alaman kamar itama tafito don kuwa komai tsaf yake acikin gidan,..

Yana murda kofar dakin sa Wayar sa ne yayi Kara
...alhamdulillah. ya furta cikin ransa tare da lunshe ido ya kwanta ruf da ciki akan gadon sa sannan ya daga wayar,

Da sallama ya fara sannan yace kaga dama ka kira ni?
Uncle bahrain yace kaifa baka da hakuri mohan,i was soo busy yazun ko gida nima ban shiga ba yace..mohan
Lpya kuwa..?ai hankali na ya tashi ban taba ganin miscalds dinka Kamar haka ba.

Wani ajiyan zuciya mohan din yayi going straight foward yace
bahrain a gaskiya mum tana bani matsala
...i realy need help,ita fa fushi take yi dani sosai.

Uncle bahar yace kai mohan..relax mana,kaba ta lokaci she wll be alright..

Cikin damuwa mohn yace no"..bbu batun bata lokaci nan ya gaya masa dan kadan daga abunda ya faru da abunda yau tayi masa a ofiice

Shikan sa uncle bahrain bai yi tsammanin karamin issure haka zai dawo wani babban al'amari ba.

Hakuri kawai yake bada mohan Din Hade Da bashi karfin gwiwa

Shikuwa Mohan anan ya sake ransa ya fitar da abubwan aransa.
"ni gaskiya ina jin kunyar kai wannan maganan gaban dad . Yanzu haka bazan boye maka ba mum ta sa na farajin kamar wani abun kunya na aikata...

Ji tayi andafa ta bazata sai ta juyo, nimrah tagani agefen su
Tace Ya bakije kin wanke aman ba,

baby ai xai kula da MM din ko?kanta ta sauke kasa tadan daure fuska..Murmushi nimrah tayi,Sai ya juyo referring to nimrahn yace Kinyi amai ne?tace yeah Tayi nuni da jikin Banafsha she was helping me kaga har na mata ajiki...

Hmmm Kawai Yace ya tabe baki Ya kalle Banafshan da gefen ido he perfectly feel her tears yasan kishina damun ta sosai,
Kyabe baki yayi unavoidably cikin ranshi yace xanyi
Maganin ki kuwa wait till i have ur time.

Nimrah tace Kije ki mana...Sai sannan Ta daure tace A'a anty ni Zan tafi da babyn ne I think u ain't well irin shi ya kula da ke ya bani kaya Na,a sakalce
Tace ...yaya mohan...batare Daya juya Ya kalle ta ba yace im taking her with me Kiyi tafiyar ki..

Ya wuce ya barsu anan duka biyu..
Itama Bata kara cewa uffan ba A hakan ta juya Ta nufi sama

Shewa Nimrah Tayo Ta xauna kan kujera tana sheke dariya mai tafe da sanyin mugun ta..Ive roll a nice dice,daMa na fada da kafanki zaki Shigo hannu na dan kinyi kadan kifi karfi na walhy...muje xuwa Ni xan rubuta ranar mutuwar ki agidan nan ...taja tsaki

Tunda Nimrah tafara kawo sabon salon rigimar cewa tana dauke da cikin sa Agidan Banafsha

bata sake iya bacci ba,

Haka ta sake cuna mata bakarTakaici aranta cewa Yanzun itama turn din ta ne Kuma dole ta samu kulawar mohan fiye da kowa agidan....

Tun tanayi Banafsha na ita daurewa har ta fara na fushi Domin kuwa kishin mijin ta ne boro boro Yake dawainiya Da ita

Gashi baya Son kula ta,Ranar data fara zuwa dakin sa Dauko baby maysam da bakin hali ya kora Ta tayi waje Tana kuka.....

Sai da Har ya gama danne dannen sa ya Dauko babyn ya taho Da ita.. tsaban damuwa Tana zaune bakin gadon amma bata ma san ya shigo ba,a gefe da ita ya aje babyn ya juya xai fice.

Da wani irin murya mai shiga rai ta juyo Zai murda kofa Tayi sauri tace yayah...yah mohan

Sai ya tsaya chak Bai juyo ba,dan har cikin Kokon ransa yake jin zafin abun da ke faruwa tsakanin su....Shi tunda Nimrah ta fada masa tana da cikin shi baiji kamar yadda yaji ranar da banafsha tayi nata ba, sai yaji Wani banbancin Feelings din dayake ma Banafshan sama kowa da kowace mace a fadin duniya

Sosai yake Jin wutar kaunar ta Aranshi,baisan Ma yaushe yyi nisa Da son ta har haka. .

Tace dama Inaso naje gida a gobe ne...Ko xan iya tafiya

Acikin ransa He was like what?Bama hakuri zata Bani ba maganan zuwa gida take? jiyowa yayi ya kalle ta sannan yace ban yarda ba..Ya juya ya barta anan tsaye

Cikin kwana biyun Babyn Sa dayake Zuwa dubawan ma Sai ya rage.Ya fara bada nimrah time dinsa sabida zagewar data keyi cikin kissa

Haka ta kona banafshn Da makirci kala kala wani bin Banafsha zatayi abinci amma nimrah zata sa mohan ya debo mata taci Tana fade fade.... wani abun Sun yana sane Sarai amma sai ya dauke kai Kamar baisan sunayi ba.

Ranar friday ya tafi dubai bai ko sanar da ita ba

xuwa wani special consultancy a german center bremen cardiologist center duka duka weekend Din sa anan yayi niyyar cinyewa...

Sai sannan data ga baya gidan Kuma Nimrah ta ware kafa da yawo Wani bin bata dawowa Gidan

Xaman ta shirun yasa taji nitsuwa ya fara shigo mata...But Ta rasa yadda zatayi Ta Kamo Bakin zaren har ta warware...

Yawan kukan data keyi Akansa yasa ta yarda dacewa tana son shi kuma kishin sa take ji.but what sHud i do? Sai ta tambaye kanta..many times xata rubuta sako Ta tura ma fazila ko Maryam Amma tun kafin su gani sai ta goge,gani take idan tafada ta fallasa sirrin auren ta....

Kunyar furta wasu abubuwan ya hanata ko wajen kawo tunanin fada ma hjy mamah Wani abun ...gashi Sun xage suna kokarin cika ta da kayan gyaran mata
Duk sha'awan shi Da kewar sa ajikin ta na cizon ta,komai suka samo Mai kyau da armashi Haka zataga an kawo mata Tayi using...
Har hjyan birni nacewa Ai dan nabar niger ne da ba haka ba.....

Bangaren nimrah kuwa bayan Ta gama Zaga kan kawaye da boasting,a yadda take fadan halin data jefa Banafsha aciki kwana biyu shi xai tabbatar data sane da duk Motsin ta agidan

Ana washe Gari Monday ranar sunday da safe Tasan mohan zai Iya dawowa the next day sai ta shirya taje gidan lady zineta.

Ita tunda safeenah tace mata ladY Z tana gida take shakkar ZUwa ta fada mata tana da ciki

Tasan halin ta sarai,kuma ayadda taga game din ta na Tafiya dai dai so take by all means ta haifo abun cikin ta..

Tunda taje gidan Suke hira da Hasinah,ita ta dada karfafa mata gwiwa sukaje suka fada ma Lady cewa tana da ciki"

Itaki lady z Kallon ta kawai tayi ta tabe baki,

"tace Allah ya raba Ipya,so long as kinsan me kikeyi makanki ai bazai dameni ba..

Tace mum dama abunda yasa nazo kenan I want to talk to you about it mum ina so na haihu i want this baby".

'Wani Tsura mata ido Lady Tayi ta sake wata shegiyar irritating Smirk..
....Tace hmmm Nimrah kenan To waya rike Ki Ne,Hasina tell her to do what eva she feel with her life,kin ganni nan inada business dina ina da mukamai A duniya and morst importantly I have all What i want..Dan kin rasa mohan Kuma to menene...?Mswww.

Daga jin haka wani Kallon Kallon Su kayi exchanging ita da hasinah sai tamata ido

A hazarce Nimrahn ta rusuna gaban ta tace noo mum bazan rasa shi ba
Dan Allah Ki taimake ni Kisa goddess Ta barmin wannan cikin,..i promise daga shi shikenan baxan sake ba,Duk wanda nayi zata cigaba da dauka i swear.. mum pls dan Allah kisa baki abar Min wannan,kinji? cike da xakuwa da damuwa ta fada. While Lady ko kallon ta batayi ba..

hasinah zata sa baki lady ta daga hannu Tace ke tashi ki kalle ni..

A sadade ta mike kanta aKasa,tace nimrah Komai kina daukar sa Wasa sabida ke dakikiya ce ko?
Ke kanki kinsan babu aikin daya bada goddess dina Wahala kamar hada mutacciyar soyayyar Ki azuciyan yaron nan..sau nawa zata fada Miki cewa That guy is not even ur Natural destiny, SHine Zaki haifu dashi sabida bakida hankali..meye Goddess ta taba roka wajen ki Inba koyin dake mahaifan ki ba?ke mexakiyi da da nema?shine yanzun zaki toxarta mu?Ure insulting me fa... Am Just tired oF your Foolishness Rashin jin ki yafara isata nimrah

Wani lumui Nimrah fuskan ta ba alaman jin dadi"cikin ranta tqce ai sai da na fada da kyar mum ta Amince Na rike cikin nan.."

Tace to ya kenan mumy,kinga fa nagaya ma mohan ina da cikin sa

Tace oho ,tsoron shi kikeji ne? Just go and abort it Kawai,ko ki mance da auren ki naki. ke kanki kinsani kina haihuwa kun rabu kenan har abada Ba boka ko tsafin da xai iya Yadawo miki da shi...

Sabida haka Kije yau dinannan ki aikata karma yayi Kwari goddess ta bata rai dake
Im your mother,ni bana son Fushin ta ya sauka akanki,Ni zan baki kwaryan daxaji xuba jinin aciki,oya Ku fita ku bani waje ni zan huta..

Duka suka ce ok,sukayi waje daya nabin daya

..Tunda suka bar nan Hasinah tunani Take,ita har yau Bata gajiya da jinjina ma son kai da mugun hali irin na Lady zineta..
 Tace nimrah yanzu kenan zaki zubar da cikin nan? Gaskiya bazan ji miki dadi ba..

Dariya nimrah tayi mai ban mamaki tace...relax hassis Kinsan ance idan anace ma mutum wawa
Wata rana Wawan yake Zamowa amma Ni ta dabance i just got an idea
Hasina tace whats that kenan"

Nimrah tace I wil Abort This baby..irin serial abortion Din nan inda bazai fita akan lokaci ba sai Na ingixa Shi da kaina...

Sake numfashin ta tayi ta mike tsayi tana murMushi"tace hassis lokaci yayi da zan jefo Tsuntsu Hudu da Dutse Guda.

Cikin nazari hasina ta mike tsaye itama Tace mekike nufi kenan?

Tace"xan zubda ciki amma ita zata Dauki alhakin sa,I Just want to blame her For this,xan mata Kullalen sharrin da sai mohan ya jefar ta Agidan sa waje Goben nan.
Hasinah tace hmm

"Kinsan zatace zatayi zuciya ko hasiss, kinga Daga nan zan gaya ma mum asan ya za'ayi da ita ko mohan baxai sake ganin ta a duniya ba,U see,i will have my mohan alone mum kuma zata yabe ni sosai..as simple as that sukayi dariya suka tafa da hasinah...

"...agida kuma Banafsha Na barci bayan Azahar Kawai sai Taji an taba ta bude idon da zatayi sai taga mahaifiyar ta Zaune kusa da ita a tsananin firgice ta mike tana cewa mamah?
 Shiru tayi tana Mata murmushi Har sanda taga ta nitsu ta shigo hankalin ta,she knew she is just dreaming amma wani abu nagaya mata ta sake abunda ke ranta Ma kurwan mahaifiyar ta Ko zataji sauki....ai kuwa kamar an kunna Ta ta shiga bayanin yadda take ji Aranta har tana mata kuka.

Babu komai A kalaman nata sai tsananin son Datake ma mijin ta da yadda ta rasa samun mafita ma matsalolin ta,
Kurwan dr arjumand baya Ko motsawa Banda murmushi Babu komai kan fuskan ta...

Cahn ta kifta mata ido slowly and calmly kamar tana fada mata sako akan ta kwantar da hankalin ta Komai zai wuce
...tana bude ido sai bata karah gane kanta ba Daga nan taji ta fado kasa tim daga kan gado,tace inalillhi Wa inna ilahi rajiun..ga wani ihu Da baby maysam keyi kamar zata tsaga kanta

A tsorace Ta dago ta ta rungume ta sai wani yarrrr take ji tsikan jikin ta na tashi,.

Takasa gane Ma'anan mafarkin ko ince idayar,smiling face din mahaifiyarta ke mata ziriya a ido tana tunowa da kuma yadda ta bata assurance da murmushi n ta cewa komai zai wuce

 ganin tunanin yana neman mata over Ga tsoro ya shige ta,Tasan Ko yana nan bazai bata izinin fita ko ina ba amma Sai taurin kai yadebe ta Tayi sauri ta shirya ta nufi gidan su maryam#surayyahmsFollow@
#SURAYYAHMS

🍒🌺AJALIN SO🍒🌺

WATTPAD SURAYYAHMS

Brilliant writers association

50 medicine

Tun daga fitar ta ta kira layin maryam tace mata tana nan A hanyar zuwa maryam Tace Toh Kizo gidan ummah Kawai ina wajen

Nan Din ta wuce driver ya aje ta,
Bakowa harabar gidan Sai ta shigo Falo da sallamar ta,Maryam din ne a zaune Ganin ta yasa ta mike da fara'a tana cewa maraba Da xuwa, ta bata wajen zama
..gidan shiru kamar ba kowa sai su biyun...aje maysam Banafsha tayi gefe tana sauke boyayyen ajiyan zuciya Don har wani iska na daban ta ke ji naratsa ta

Maryam tace kaga amaryan doc hjy Banafsha...,sai wani pale pale kike kinyi haske, Banafsha anya ba wani katon kwallon kika chabe ba?

Murmurshi kawai tayi tace wannan ai sai ku yaushe zan iya mantawa da azaban danaci a nakuda?

,. . yah Yaya ameer ango na Fatan kuna lpya?

maryam Tayi Murmushi tace lpya Lau fatan dai zaki zo min, dan nan dai ba gida na bane.....sukayi dariya Banafsha tace Ke kadai ce?naga bakowa Inche Lpy?

..tace eh fa daga shiga kitchen nafito sai banga ummah ba,bari dai na duba mana abincin sai naxo..

Sai Ta gyada mata kai,bby maysam ke Neman fara kuka sai ta dago ta ta aje ta kan cinya tana bata nono

,...yadda yarinyar tayi shiru ta nitsu tana tsotsar ta sai ya sa takafe ta da ido tana ganin kamannin mijin ta,.ranar ma tanaji hajy na fada cewa mohan bai wani sha nonon uwa ba sabida hjy mahnoor ba ita ta raine shi ba
...tace hjy mahnoor ta samu cikin shi ne a lokacin da take kokarin fara kafa career ta na fashion and desing a duniya kuma tana so yayi karfi sai kawai ta fi bada muhimmanci achan fiye da shi.

Sometimes idan hjy na bada labarin yarantar sa har abun dariya yake bata,yanzun ma wani abun ta tuno zatayi dariyan amma saiga hawaye sun sako mata

...wani mugun mugun son mijin ta da kewar sa ke neman mata illah,'dan kadan tahade goshin ta dana maysam tana kallon kamannin sa anan tana kukan zuci.

Maryam Tray din hannun ta ta aje Ra karaso kusa kanta tace Banafsha?...
Bata ma ji ma ta kuma cewa
nafsha... adan firgit ta dago cikin sauri Ta kuma sadda kai tana goge hawayen ta

..maryam da shiKe ta dade tsaye kusa da bayan ta tana kallon abunda take tuntini tuni ta karbe baby ta ajiye gefe ta Dawo ta tsuguno gaban ta

tace Banafsha Ipya kuwa,meya sameki kike kuka? Bata Amsa ba Tayi shiru...ko maysam ne bata da Ipya Kin fada ma doc?what's going on....

Da maryam ke tambayar ta A haka sai taji She cudnt hold it anymore,wani matsanancin kuka ta fashe da shi tana cewa babu komai kawai wani abu nake tunawa..sai kuma tayi shiru Ta cigaba ..hankalin maryam Kuwa tuni ya tashi,but she's very tactfull dan haka ta nitsu ta riko hannun Banafshan gently Tace kawata"..kar kice min iyayen ki kike tunawa...ko su hjy sun bata miki rai ne?...Tayi saurin girgiza kai

tace ah'a Maryam...tun daga nan bata Sake cewa komai sai kuka...

Gefe da ita maryam ta Dawo zauna ta jawo ta jikin ta Tafara rarrashin ta,Maryam duk wani kalma na hakuri ta fada mata da kyar ta dago Ta hadiye kukan tace Mata maryam Im not happy....my marriage,... ni bansan ya zanyi Da shi ba,It s alwys hurting Me..what shud i do pls..?

sosai maryam ta shiga halin tausayin ta Data ganta a hakan ayanda suke rike da amincin junan su itama tuni ruwan hawaye ya taro a idanun ta,tace Banafsha dama yaya mohan ne?Kar kice mun fada kikayi da shi,Pls talk to me Nasan ki da boye damuwa Aranki,Kuma ba yadda xaki rike abu aranki ki samu saukin shi...pls whats wrong?meya faru ne nafsha kefa ta Yaya Mohan ne shi kadai, shima naki ne ke kadai.

Cikin shessheka Banafsha Tace ah'a kam, yaH mohan baya ma kula ni yanzu Ni tunda na haifi maysam na dena gane kansa,i just wonder if he care about me or not he changed alot ....i think he doesn't like me Anymore..Dan yamin abu nayi fushi Then he dosnt want to talk to me again,kuma wallhy ina son shi Bazan iya jure hakan ba..

Yanzun haka anty Nimrah tanada ciki,hanklin sa gaba daya yake so ya maida shi chan..naga ko maysam din ma yana so ya dena kulawa Da ita kamar da.
.shikenan Ni Sai na dawo musu hoto agidan Ko?
Wani kukan ta saki Ta hade kanta da gwiwa,
.
Maryam sai ta danyi shiru chan ta kalle ta tace toh kiyi hakuri Banafsha,but i can't believe that

haka kawai yaya mohan zai canza miki bayan kin haihu masa..,ni a yadda nake gani yake tarairayar ki gaskiya inaga kinyi masa wani abu ne.. So fada min..Banafsha me kika masa?

Dagowa tayi kamar zatayi Magana amma sai tayi shiru

Maryam tace "look Kar kiyi min shirun nan naki, idan ma baki sani ba we have to think right now,bazan iya barinki acikin kuncin nan ba..

Banafsha Share hawayen ta tayi
Ta gyara zama tace inaga Fa tun akan lokacin da nafara nakuda ne,anan tayi highlighting ma maryam abubuwan da suka faru,ta Karashe da cewa ni Da farko dai sai naga kamar babyn sa Dama ya so bani ba...maryam what do you think am realy confused About him,kuma fa kinji abunda anty nimrah tace min
...kafin maryam tace zatayi magana sai su kaji gyaran murya akansu

Ummahn ta ne tafito daga bayan gida a daki, toh data jiyo abunda Banafsha ke fada sai taki tayi interupting dinsu
Komai aka fade shi a kunnen ta..

Banafsha A sanyaye ta rusuna tace ina wuni ummah ashe kina ciki..

Ummah da tuni tadade da shiga kundun nazarin abun da tajin bata ko amsa ta ba A masife tace Mena ke ji haka Banafsha,dama A haka kike rike auren ki?ashe ni ba uwa bace da baxaki kawo damuwar ki waje na ba?

..wani hawayen ne suka zubo mata kirjin ta na Bugu,.. tace ummah Kiyi hakuri, baya bari na fita ko ina Ne yau ma dan baya kasar ne na fito Bai ma sani ba"
...ummah tace yimin shiru awajen,ai kin bata min rai Banafsha,
Banso naji haka daga gareki ba.

nan ta hada su Biyun tayi musu fada tana cewa bawani uxurin da kuke dashi a wannan lokaci,

ure just 16-17 ai tunda kuruciyar ku zaku ji dadin aure ba sai jikin ku yayi nauyi ba,

ga yan mata nan ire iren ku sun bude ido sunsan meye duniya take ciki
'Yara yan 16-20 duk ina ganin su suna xuwa nan siyan kayan gyara,wani bin mu manya ma sai su nemi sufi karfin mu Ta Fannin Rike miji da tattalin shi,amma wai ku da kuke yara na Har zaku zauna kuna shirme ana cin tuwo akanku haka?
..Banafsha ko dai baki son shi ne?

Tace ah'a ummah,..ina .... son shi..

Ummah tace Banga alama ba, To tashi maza ki biyoni daki, ke kuma maryam ki kula min da jika

na.. tace toh ummah.

Ayayin da Banafsha ta bi bayan ta daki ummah tana zama Banafsha ta nemi Waje itama kusa da ita ta zauna A kasa ta sunkuyar da kai..

Dan shiru ummah tayi tana kallon ta,cikin nitsuwa da lallashi tace,ba fada nake miki ba yata Share hawayen ki muyi magana ki dena kuka kinji!?

A hankali ta dago jajayen idanun ta tace kiyi hakuri ummah nasan nayi kuskure Aure na ya lalace min.. wallhy bansan yazanyi bane Shiyasa.

Ummah tace um um Banafsha Kidena fadin baki san ya zakiyi ba...,ke kuma fisabillahi haka akeyi!? Da kika haihun shi yafada miki baya sane dake?ai Wanda yaso abunda ka haifa yana son ka Ne..Wato ke duk wannan baki gani ba ko, kishi zakiyi har da Yar cikin ki?Banafsha Lafewa tayi kadan ta sharo fuskan ta Cikin jin kunya

...."umma ta cigaba da Cewa haba Banafsha ta, Ina kike kai tunanin ki Ne? kefa Ya mace ce,keda nake ganin kwarjinin ki afili ashe har akwai kishiyar da zata xuga ki Kiji ta? yanzu fa kin girma, ke ba yarinya bace da zaki tsaya ki kafa hujja da maganan kishiyar ki kowa takansa yake a gidan miji ko cemiki Tayi Ita bata Kishin shi?,mijin ki might be having problem somewhere else wanda baya son ya shafe ki a condition din da kike a lokacin da kika haihu,kece yaka mata ki dinga bada uxuri kafin ki yanke masa hukunci,shi aure ai ba wasa bane he is ur life partner,alwys stay put and be open to him Kifadi masa damuwr ki,kar kiyi shiru da abu aranki dan wata rana zaki tafka mummanan kuskure.

Sannan The very next time naji kin korashi ajikin ki da sunan kina fushi dashi har gidan zanzo na same Ki naci kaniyar ki,dan baki da hankali Mijin kin xaki raba gado da shi wayace miki ana haka..

Ummah tace,Toh kar nakara jin kinyi hakan dai, don ba tarbiyar mace mai kamala bane,..aure ai bautan Allah ne don haka bason ranki zaKi rikayi ba,maza ki sa ma zuciyan ki ruwan sanyi ki san me kikeyi
go back to your man now, ki bashi hakuri kar ki yadda Ki kyale shi har sai ya hakura

Dan Siririn hawayen ta ta share Kafin tayi magana umma tace Oya Tashi kije ki dauko maysam kizo..ina tana dai karban nonon ki da kyau tace eh ummah
",yawwa to dauko ta..
A sadade ta mike ta fice kafin ta dawo ummah ta fito dawasu special packages daga cikin kayyakin siyarwan ta Ta aje Domin ta,tace goya ta maza ki koma gidan ki kar ki kara makanki laifi,Babu kyau fitowa haka kibari yabaki izini Sai kizo kuyi hiran ku

Tace toh ummah nagode...

"nan ummah ta debo kayan tace Ungo karbi Wannan Turaren da kin gama wanka kizuba a clean water ki shiga ciki na minti 10,Ga Kuma wannan kije ki shanye yau da gobe duk sun ishe ki..Banafsha Abun ta karba tana juyawa a hannu Wani hadin kutungwila na pure zuma dabino kwakwa da sauran hadin da bata san me ajiki ba,ansa shi well packaged agoran yoghurt tsaban Abun ya tsumu har oil Din fruits din kwakwan dake jiki na kama goran gashi coffe brown Yana gamshin dadi kamar Wani Yummy chokolate,sai wasu tsumin Suma agora anma tace mata kar ta bari Ya kwana ta shanye shi A yau Din..

Banafsha Har bata san kalman da zatayi godiyan da shi ba Don kuwa sosai taji sanyi aranta

,rarrashin ta ummahn maryam ta Dada yi zuciyan ta cike da tausayin ta"
tunanin ta itama shine yanzu da ace bata duniya wazai rike mata mata nata yar?

Ko da taga Yanayin rayuwar Banafsha da sauran Kananan Yara Irin ta wanda Suke rayuwar auren Kuma Basu da uwa a duniya,

takan jinjina masu Sosai tasan Hrdly suke sanin inda xasu aje kansu a kafadar wani suyi kukan damuwar su..

Haka Banafsha tayi sallama da su ta koma gidan ta ko kiran driver ma bata yi...'

'Wanka ta fada tayi sallahn magrib,tunda ta samu taci abinci kadan ta shiga kundun tunanin abunda ummah tace

.. After 9 na dare ta kwantar da maysam,abubuwan da ummah ta bata ta shanye sannan ta bi gado n ta ta kwanta,

Ji Take kamar ta gama saita tunanin ta akan komai,Sai dai har yanzu Tunanin salo da yadda zata bi ta bashi hakuri ke damun ta, by 8am na safe dama ranar monday ne a tsanake ta gama komai har ta yi breakfast ta shirya maysam cikin all white baby set na jimmy chuu yarinya ta fito angelic as usual

Tunda tayi amfani da turaren wanka da umma ta bata qamshi ne kebin ta a dik inda ta tashi ko ta zauna"

Da safen Dakin sa ta nufa ta bude tana kallo Daga bakin kofa,

 kwana biyu da bata zuwa nan akai akai sai da taga banbanci

 nan ta shiga kintsawa tana buge kura,within some minutes ta share ko ina ta goge, wani hadadden bedding set ta fito da shi pure sea blue mai laushi ta shinfede gadon sa da shi,bata fice ba sanda ta tabbata har toilet din dakin na qamshi da sheki

Sai chan da yamma wajen karfe 3 saura taji driver ya ce shi xai je dauko
Shi a airport...

nan ma ta sake wanka ta shirya kanta cikin wani pingelin gown marar hannu pink da ita babyn
Ta suka zauna a daki..

Bata sani ba ashe tana shigowa daki Nimrah ma ta shigo gidan

agurguje ta haura sama Dan dama ta riga ta gama setting plan din ta. .

Dakin mohan ta fara lekawa Taga ko ya dawo ganin an sauya komai an tsaftace yasa ta fashe da dariyar mugun ta"irin wato har anzo dubawa ko ya dawo ko?
Tabe baki tayi ta Shigo
A Kan kujeran dakin ta zauna ta aje wani magani In form of pill akan stool nesa da ita

..,dama wanda tasha na abortion din already ya fara aikin sa tuntuni Don har ta fara serial bleeding,dama lab scientist din ladyn tace mata muddin ta sha wancan karamin pill din jinin zai zubo mata dayawa har yabi kafar ta and is very risky duk da haka bata damu ba..

Wayar ta ta daga ta kira faisal,shi sam baya son muamala da ita amma tsoron ta yake ji,.
nan ta tanbaye shi inda mohan yake,shi ya kayyade mata
Cewa nan da minti goma ma driver zai iya shigowa da shi Gidan,

Tana katse wayar ta mike ta bude kofar dakin San
sai ta wani irin sake shi da karfi yayi kara kamar an shigo ne aka rufe....

Sau biyu tayi hakan,kafin Banafsha ta ji,Ita Kuma sai ta dauka ko shine ya dawo

ba wani bata lokaci ta taso dan ta zo ta tabbatar Da hakan,

Wani malak nimrah ta kwanta kan cushion dinsa ta sake takalma da jakan ta akasa ta riko cikin ta tana wash wash,..

Wani dada kara sautin nishin ta tayi ta rikota kasa musamman data ji sallamar ta...

Itako Banafsha mamaki da tsoro ne ya cikata,tace antyy lpya kuwa. .?

Wani munafukin
Kuka nimrah ta sake,tace ciki na kemin ciwo Banafsha .. Can you Pls help Me ga magani na chan dauko min nasha.

Arude Banafsha tace ok, sai ta aje babyn ta akan gadon sa ta dauko pill din,

gefen condenser tabi ta tsiyayo ruwa ta zo gaban ta rusuna tace sannu anty ga shi nan na kawo miki,

Ba laifi Nimrah ta karba ta hadiye agaban ta Tasha ruwa.

Cup din ta mika mata tana rike dashi tana kallon yadda take wash washhhh,jim kadan kawai Nimrah tasa ihu sai zirrrrr jini yafara bin kafar ta.

A rude Banafsha tadafa kafadan ta tana furta innalillahi wa enna ilaihi rajiun..sorry sannu

Nimrah Tace sake debo min ruwan zansha,ba jira ta mike tana dawo mata da ruwan,Ta karba ta sha..

Cikin tausayawa Banafsha tace
Anty Ko na kira driver akaiki asibiti"

Dan gyara zama nimrah tayi Ta Kalle Banafshan,

"ita dama already anyi inducing mata pain reliever,duk murde murden munafirci take Kawai dan ta zulma ta, tana jin zafin Dai amma is bearable"Sai tace bazan je asibiti ba sai dai Za'a Akaiki,dan kuwa yanzu xaki samo Ciwon tabin hankali

Cike da mamaki Banafsha tace mene?Ki kace me

Nimrah tayi dariya tace Yes u heard me Right,Dago rigan ta kadan tayi ta Gwada ma banafsha jinin Dake bin ta. ,tace Wawiya Kawai Toh This is all planed Dama so nake Kisan kin bani magani da hannun ki...,Ni zan fada ma Mohan kin bani maganin zubda ciki a ruwa Nasha Cikin da yayi min ya xube,

So mrs Banafsha Can you Deny it?tayi dariya Mai shake da tsegeran ci

Ganin Banafsha ta shiga shock tayi durus Cikin rashin sanin Zatace, yasa ta kyabe baki Tace

"ki ce masa karya ne Mana, or are you two fighting?ta sake fashewa da dariya,

well basai kin amsa ni ba nasan komai tunda nina hada ku,amma kinsan makomar ko kuwa? mohan Zai ki ya yarda dake sai ki dawo mahaukaciya Ya kora ki agidan sa. .simple.

"nan Banafsha ta dago kai Wasu takurarrun zufa ne suka fetso mata Cikin tsananin mamaki ta sake karamar dariyar takaici tace
Hmmm Heheheh"

..Lallai fa, So What do you mean now anty?kina nufin sharri Za kiyi min Yanzu yanzun nan ko? Toh Menayi Miki haka? Ko duk sabida yaya mohan ne? I tot ure in pain Ni sam ban fahimce ki ba Fa are you for real?..,Tayi kwafa ta na kallon nimrahn Kanta har na mata kaikayi

Nimrah tace i am,ba wasa nake miki ba,kwanan ki ne ya kare..gwara Ki Sake ki fadi abunda ke ranki Don gida na xaki bari yau,.

Idanun Banafsha take sukayi ja cikin rawan murya tace akan me?zamanki nake ne..

Nimrah tace ai ba mai zamani Dani dama,I have neva liked you Kuma kin sani,dokar zama na dake shine duk abunda zanyi na tarwatsa rayuwar ki sai nayi shi.....

Wasu hawaye Masu zafi ne suka sauko mata tace anty Shine Har da kashe dan cikin ki?Ure this wicked? No wonder kikace yaya baya so Na abun ciki na yake so,so it was all your plan right. Muryan ta har na rawa ta karashe

Wani dariya Nimrah tayi tace Hmmmm Banafsha kenan Ure dump,stupid blind..Wato wannan kawai kika sani ko?It's ok,wasa Dai ya kare Kinga wanda yaci baya zaiyi ouuuuut...

A zafafe banafsha tace Wallhy Baki isa ba,munafuka kawai"Allah ya tuno asirin ki,ashe Dama hada mu kawai kike dan ki raba ni da shi?

"Basar da harzukan tan Nimrah tayi tace
Deny it Mana bake kika Ban magani nasha ba?

Wani Kukan Fushi da takaici Banafsha ta fashe da Shi Cikin ranta ji take kamar Ta kashe Nimrah dama ashe Haka take?
Tace toh,In na fice Anan ai zanga wa zaki lakama sharrin akace Miki kike kadai kike da bakin sharri,zan fita kuma ba Wanda ya isa yace nazo nan na baki wani abu

Banafsha nasa kafa Nimrah ta shake ta

Charaf sai suka ji sallamar sa
Wani Ihu Nimrah ta sa Tace wallhy baki isa ba Sai kin fada min meyey kika saka min aruwan ciki na ya xube

Wani baru jikin Banafsha Keyi kuMa ita ce ta fara daga ido ta kalle shi shima Kuma kallon ta yayi

Kai Lpyar ku kuwa?Ya fada da dagon murya Yana kallon yanayin su...

Cikin wani munafukin kuka mai kunshe da sinadaran makirci Nimrah tace Mohan na shiga uku,ohhh thank god ure here, wallhy

Matar ka zata kashe ni.

Cikin kuka Banafsha Ma tace karya kikeyi zaki kashe kanki dai

Wani sake baki Nimrah tayi har yana bari Yana zubda yawo, tace Daga cewa ta taimake ni tabani pcm shine zata hado min da wani maganin?

Cikin kukan tace mohan Look at me,i don't know what's happening Sai bleeding nakeyi,mohan i think lost my baby ..jinin dake bin kafar ta talakato a tafin hannun ta tana kukan fitan rai tana kallon shi kamar ta zare.

Tunda Banafsha taji me take cewa ta shiga shock Tana kuka bata farfado ba A durus ta tsaya ta waro ido tana kallon nimrah ji take kamar Komai a film

"anty Ki kace Ni Banafsha na baki wani magani?Ta iso gaban ta a hargitse,are you mad or something?Inaga fa baki da lpya ke Ki fada masa abunda kika ce min Mana?
Why are you implicating me For god sake

Sai Ta dawo gaban sa tace
Yayah She's lying To you,ai tace plan takeyi Dan ta raba ni da kai, yanzun nan Fa Ta ce na bata magani bata jin dadi what will i gain da har zan baki maganin zubda ciki..? A mugun fusace Banafsha ta fada dan bata masan ta fada ba,.

Mohan shiru yayi yana mamakin su,he was like so sun ma zubar da cikin?

Banafsha kuwa kirjin tane ke bugu tuni taji hankalin taya tashi dayayi mata shirun

Ga Nimrah sai tsuma take Agaban su tanacewa cikin ta cikin ta ancuce ta

Cikin takaici mai tafe da bacin rai,Tace Kema Baxaki fa fada masa gaskiya Bako? ni bansan meke damun ki ba kuma baxan dauki alhakin komai ba

A haukace Nimrah tace shut up bitch,muguwa kawai azzaluma wallhy nafi karfin munafurckin Banafsha

u cannot cheat me twice,ga asaran ciki ga munafurci da karya ?yaushe nayi miki magana

Ai dama nasan baki kaunata,komai xaki iya cewa,Wato dan kin san nafiki gindin da zai haifo Da namiji shine bari ki cika mumman burin ki akai na ko?

Wani yunkuri Nimrah tayi kamar zata tashi ta cahkomo Banafshan sai kuma ta xube akasa ta kara sa da ihu tuni jinin ya fetso sai gashi tafara karkawa

"Shikam tsaban mamakin su sai ya zamto musu dan kallo,nimrah najin jiki amma haka ta zake tana cewa Banafsha ta zubar mata da ciki dan bakin cikin zata haifo da namiji..

haka itama Banafsha ta zage tana cewa bata san da hakan ba,karshe kuka Kawai ta fashe da shi Bata iya cewa Komai
Nimrah ta xautar da ita tasa ta bayani har makokoron ta na mata zafi Har ciwo kanta ya soma yi tasan inda da halin da zuciyar ta zai fado kasa Shima da tuni ya sauko,

Yana shiru

Sai da suka gama musun su Sukayi shiru,ya tsuguna gaban Nimrah yana observing zuban jini,

kafafun ta ya dan ware kadan sai ya ciro handkerchief daga aljihun sa ya dan share jinin da suke biyo sawun kafar ta
Ya Bashi critical look...

Dan sosai Ya dago furucin kowa gani yake kamar Yasan mai gaskiyan acikin su

Nimrah Sai wani washhh washhh take,cikin kuka tana cewa wallhy bazata yarda ba.

sai ya daga ido ya kalle ta yace Nimrah relax Pls zan kira aliyu yanzu yaduba ki ,ko kinajin jiri ne?,tace ba sosai ba Kuma wallhy sai ta biyani baby na..yace to ki nitsu kifada minene ya faru Kar kuma naji Muryan kuka

Nan ta sauya kama kamar tsohuwar makira tace"..naxo gida kaina na ciwo nace ta taimaka min da pcm bansan me tayi ba daga nasha sai nafara bleeding,Ni nasan dai aruwa kika xuba mun wani abu

charaf Banafsha ta yanke maganan tace ohon miki,nidai ba abunda nayi miki kuma kema kinsa ni,Aniyar ki tabiki abunda kike so Ya faru dani bazai Faru Dani ba, mugu..wa kawai

wani mugun kallo ya dago ya bita da shi yace waya Sa bakin ki?
Ina wasa dake ko?

hawaye masu xafi ta sauke ta dauke kanta Gaba daya jikin ta na karkawa

wallhy ciki na ya zube bazan yafe miki muguwa kawai...

Yace Nimrah, its kk muje dakin ki kijira shi anan ina xuwa.

Tallafo nimran yayi akafadan sa
suka fita su ukun
Banafsha na bin su a baya gaba daya abun duniya ya dameta

Ashe dama haka take?babban munafuka,har agaba na ma tana hada min Sherri,?kawai dama tana so yaya ya daura min laifin komai ne Ya kOre ni..

Mohan Aje ta yayi akan gado,ya nemo abu ya goge ta dashi

wayar sa ya cire yayi kira aka zo aka duba ta inda Wani doctorn daban ke tabbatar masa da lallai wani magani mai karfi tasha a ruwa ya zubda mata cikin...

Alluran da aka mata Alokacin ya na sa ta layi amma Haka ta bude ido tanace masa Mohan kaji ko?

Ko likita ya fada ita ce tabani maganin Im sure acikin ruwan ne..

Banafsha sai jikin ta yayi sanyi rungume da babyn ta ba abunda take sai hawaye

....a haka Har nimrah tayi barci bai juyo ya kalle ta ba..
Maganganun da Nimrah tayi tayi yayi mummunan mata illah Acikin ranta

Ita hurts her to know that gaskiya yana gaban ta amma bazata iya bayyana Ma kowa yagane ba"

Tunanin makomar ta take Tayi A wajen mohan,Don tasan bai isa yace ua gane kan fadar sun ba,abu daya ne Kawai afili Shine Nimrah ta laka mata alhakin zuban cikiN ta

...sai da Taga ya mike xai koma dakin sa tayi sauri ta aje babyn ta biyo bayan sa...

Tace Yaya,...yaya mohan pls wait and hear me out"basar da ita yayi...bai tsaya ba sanda ya bude kofar dakin shi,..

Wasu mugayen kallo yabita da shi,a sukwane ta dago ta Kalle shi
Tace Wallhy ba haka bane ya faru,ita ta ce na bata maganin zata sha bansan niyyar ta bakenan da bazan bata ba"She said she wanted to ruin me...Allah kaji na rantse maka Sharri take min.

Cikin dakewa Yace ok doc ma yayi karya kenan?
Kin bata wani abu ki baki bata ba

Tace eh, ai shima baisan abunda ya faru ba..."Yaya kayi hakuri kar kace na xubda mata ciki wallhy banyi hakan ba

...da taga irin kallon dayake mata har kasa ta nemi silalewa tana kuka xata roke shi,hannun shi take da niyyar kamowa yayi saurin kwacewa ya hade rai,,a masife yace don't you dare touch me again,"kin dauka xan kashe kaina akan ki ne?...im not even surprise inkinyi hakan

Ba abunda kika
Ga dama shi kikeyi ba?,ok Allah ya bada sa'a,..and just get out of my sight....right now.... ya daka mata tsawa dai da ta razana taja gefe

a rude tace yaya no,pls don't take it that way wallhy walllhy karya anty takeyi min,i just helped her dan naga bata jin dadi kuma ita tace nayi mata hakan bansan mesa doct yace maka nabata magani ba..yanzu har ka yarda zan iya yin haka...?

Kukan Ta sosai yaKe Ruguza saitin brain dinshi Da shike hankalin sa da tunanin sa basu kusa Shikam Baima jin me take cewa kawai sai
Yace eh,and i said get lost bana son ganin ki nace ko?Tsaki yaja...zai rife kofa tasa hannu zata tare ko ajikin sa ya buga da hannun nata saida tayi kara Taja da baya..

Anan ta xube a kasa Tana kukan Tana tapping kofar sa Tace Yaya mohan Pls don't send me Away,kayi adalci ka ji abunda zan fada maka,yaya Mohan Pls Open the door...Kayi hakuri Kaji?Pls im sorry.

Haka tayi tayi har ta gaji tayi shiru,

ShIma Bai iya motsawa ba Tun tuni jingine yake abakin kofar ya lumshe Ido yana jiyo ta.

Banafsha Sosai ta zuciya Abun ya matukar kona mata rai,sai Shessheka take tayi shame shame akasa tana zaune A kofar dakin sa..cikin ranta take cewa yanzu ta hada ni da shi kenan?in ya kore ni A gidan sa fa?She's a devil,She used Me...
munafuka Ce kawai shegiya,makira annamimiya Muguwa bazan yafe miki Ba, kuma bazan bar gidan nan ba..
Hawayen ta ta goge tas Kasan makoshi ta Furta
Ai wallhy kuwa bata isa ba,sai ta gaya min yaushe na bata maganin xubda ciki Kona xame mata Babban fitina agidan nan..a masife ta tashi ta nufi dakin nimrah fuuh ta bangaje kofar Babu ko tsoro aranta..

Gani tayi har bacci ya debe ta,bata hakura ba dan kwata kwata bata yi tsammanin haka Asalin halin Nimrah yake ba..

Yarta ta dago ta rike sannann ta shiga kallon nimrah dake bacci tana cewa

"I was respecting you sabida na dauka kin girme ni ashe ke banza ce Baki cancanci komai daga waje na ba girman ma nafasa baki

 Kinyi kuskuren nuna min kazamin halin ki in rashin imani kike ji dashi wallhy nafi ki,..ashe har xaki Iya zubar da ciki dan kawai ki hada ni da miji na?,only god knows wHat uve been Saying to Fool me agaban sa Im sure that's not all,...toh da kina ji na da bakiji na
Ki sani kinci bashin da bazai Taba wuce Miki awuya ba,

I will teach you a lesson you won't eva forget...

Daga ni saike a Wajen yaya mohan,Daga yau sai kin gwammaci da baki Fada min Ke wacece ba bare ki hada min wannan sharrin rainin wayo,u think im a fool,toh even a fool at forty cannot be a fool forever

Uve Bring It on Ko? i will take you to the finish Insha Allah da bakin ciki na zaki bar gidan nan.

Wani zazzafn Tsaki taja a xuciye ta wuce dakin ta,akan gado ta Ajiye maysam ta Shiga rarrashin ta Har tayi bacci

Just 3months da haihuwar ta amma har yanzu babu Wani sassaucin da ya shigo mata

Mikewa tayi ta doro alwala ta yi nafila Tana rokon Allah,zuciyan ta cike take da tsoron matakin da mohan zai dauka akanta gobe,gashi ta kwallafa Son shi aran ta,ji take Kamar idan yace Ya sake ta ta bar Masa gidan zata iya zarewa.

gado Ta koma tana mai cusa kanta cikin pillow tana kukan zuci,..yau Kama tasan ranta yayi matikar baci

Ita banda tsoron Nimrah datake ji Tuntuni ba Da babu wani mumuman zargin data ke mata akan komai tsakanin su

...sai gashi Nimrah ta bata mamaki yau ta nuna mata wacece ita boro boro

Tace uhmmm,ai daga yau ko mutuwa take Na asali bana kara yarda da ita,shima Mijin da take gadara akai sai na kwace shi kuma nayi yadda naso dashi

Idanun ta har sun haura tsabn tayi kuka Juyi take ta furta,.hmmm she think she's smart ko har da cemin dump mswww,i maybe dump, but im not stupid.

Da safe ma haka ta tashi da shi aranta..Sosai tayi zuciya.,sai dai ko kadan bata jin zata hakura ta karbi defeat

 instead ma wani karfin gwiwa take ninko ma zuciyan ta nacewa lallai itama sai ta nuna ma nimrah irin mata salon kissar Komai ma yafaru bata damu ba

Shikuwa mohan Tun jiyan ya kasa aje kansa Waje daya bare ya yarda cewa Banafsha xata iyayin haka Ma Nimrah

But Wani zuciyan nace masa kar ka amince da mata kishi ma kawai yana Iya haukatar da tunanin su,su aikata komai

Ajiya cikin daren Faisal ya kira

Tun Kafin Faisal din ya shigo Sai yayi packaging Handkerchief din daya goga jinin Nimrah akai ya rufe Awani envelope

sai ya ce masa kayi Sauri ka kai ma aliyu Wannan sakon kafin ya bar asibiti.

Yace yeS sir Ya wuce Ya tafi

sako ya Zauna ya tura ma aliyun Mai dauke da Kalmomi kamar haka

"Dude,nasan xaka iya gane min siffar Wannan abortion din,I want everything In details And i want the result Today Xan jira ka a kofar gidan ka by 10ocl In ka tashi.

Daga nan Wanka yayi,ya fita agidan bai sake dawowa ba sai da 10 na dare yayi ,ya nufi wajen aliyu.

Acikin mota suka xauna ,Dr Aliyu Ya mika masa report,yace Mohan What's going on Ne?Jinin waye?

Mohan Bai Amsa Saida yagama karanta result din Ya lumshe idanun sa tare da sake ajiyan zuciya yace Aliyu Nimrah ce ta zubda ciki and she was claiming that Yar uwan tane ta zubar mata

.....AliyU yace what?Nimrahn bata da hankalin ne Da Banafsha zata bata drugs harda pill Dinshi?

Yace Bar rainin wayo, i just found Out now Dama kawai gaskiyan nake so nagani ,tace wai pcm ta bukata Sai ita kuma wancen ta bata wani..

Aliyu yayi dariya ya kada kai yace But this Result isn't saying that at all,ko ba kagani bane? Wannan Cikin nata ma anxubda Shi almost 16hrS ago..Jinin ne kawai aka ingizo

To meyasa Ita Nimrah take haka Ne?Kai mata akwai fitina wallhy

Tabe baki Mohan Yayi yace forget dama kawai nasani Ne...tayi ma kanta.

Aliyu yace pls kayi haKuri Mohan

Wata Miskilin Murmushi Ya sake yace I have to go now Saida safe Kawai Sukayi sallamah

Mohan Tunda yajI hakan hankalin sa Sai ya kwanta Sosai.

Sai dai Maimakon yayi reacting Ya nuna Musu yasan komai Sai ya basar Musamman Ma Nimrah,

sai yayi Shiru Yana kallon
Su duka kowacce da abunda take ayyanawa Domin Ya bi nata qudirin....

A ransa Yaji haushin zuban cikin amma bazaka san Da haka ba

a safiyar ranan Nimrah tayi sheme sheme tana jira yazo ya mata hidima ya kula da ita,amma sai shiru take ji har 10 Ya wuce batayi wanka ba bare taci abinci..

Mai aikin data ke kyama ita ta Koma dafa Mata shayi Ta taya ta shiga bathrum Ta tsaftace kanta

Sai tace Tunda aranar farko Ne bazata dauke abun komai ba Maybe Mohan yana bakin cikin Xuban cikin ne,Gashi ta jira taji Ko an kore Banafsha Agidan shima sai shiru

Gashi an bata 2weeks bed rest Babu fitowa

sHikuwa Tunda yasan metayi sai Motsa Motsan bakin halin shin suka Sauka A kanta gaba daya sai ta dena gane kansa

Zai Dai shigo duba ta amma sai yaga dama sannan bazai fi minti 10 ba xai fita,sometimes Na a tsaye Kuma Duk Iya kisisinan ta baiya kulawa

Shi bai rarrashe ta ba,Shi bai mata fada ba, mata komai ba sannan hannun shi baya kaiwa jikin ta da Sunan taimaka min na tashi ko zan sha ruwa

Wani bin intana fade faden ta sai yayi shiru ya tSura mata ido Ko tana koke koke Ya basar Ya juya kai yana latsa Wayar sa

Ya Gama Lura Damuwar ta kawai shine ya wulakan ta Banafshan shi,Acikin ranshi sai dai yayi murmuShi yace yarinya Ai kin makaro ita din ma ina nan A kanta...

a fannin Banafsha Sam Baya sake mata Itama,.shi tunda yaga ta kafe akan maganan Tana so ya saurare ta,sai ya fara punishing din feelings dinta,

A kullum xai Nuna kamar 100% ya na kula da Nimrah kuma yana tare da ita kodan ya bata haushi,.

Wani bin ba dakin Nimrahn yaje ba amma Inta fito zata wuce zata gansa sau dubu a kofar dakin

Daga tayi magana Tana son ganin shi sai Yace baida lokacin sauraron ta shi Nimrah bata da lpya yana kula da ita

Haka Banafsha Tayi ta danne zuciyan ta taki tayi fushi,har abun ya kai ta makura Sai ta Dena bibiyan sa

Shi baiyi hukunci ba kuma vaice Musu komai ba,nimrah ma dataga wulakncin san yayi yawa sai tayi zuciya da shi tace Ma hasis ai Banafsha ta tsafe shi Ne ta lashe masa zuciya.

Bayan kwana biyu Dayaga dukan su sun sha jinin jikin su da shi,Sai ya shirya tafiya conference abinsa

Ranar da zai tafi da safe Banafsha tana kwance da babyn agefen ta ya shigo Bata sani ba Don Sai da yakai tsakiyar dakin kafin yayi sallamah sai ta dago Kai.....

Kallon da yake mata yasa bata iya hade ido dashi ba ta gaishe sa Cikin sanyin murya

Gaban shi na yawan faduwa aduk sanda yaga fargaba a fuskan ta Yace ki shirya,gobe zakije gida...bayan kwana biyu zamu zo.

Wani garas taji maganan ya sauka a kunnen ta Tace "Ya Allah, ko dai korata Yaya mohan yake so yayi?. ,Tuni sai taji Bugun zuciya

a gaskiya bata so taje ko ina ta barshi agidan da Nimrah,
Tace yaya mezan je yi agida? Why not na jira mu tafi tare da kai.

Yace a'a..haka Kuma yaki fir karshe ma Data takura sai yace Kawai ta tafi shixai kula da matar sa ne..

Abun ya mata ciwo Haka ta kwana da maganan aranta Tana jiyawa,da safe Data farka gani tayi an dora maysam black diamond brace a wuya mai shape din love mai kyau Tsadadae

data bude sai taga Hoton shine da na babyn sa aciki
Murmushi ta
danyi Tana kallon yadda sukayi kyau,sai ta Shiga kimtsa Kanta Amma da niyyar babu inda zataje sai Da shi

Tana sane da bayanin family function din da aka shirya gaba daya familyn za'ayi,Dama hajy tace on 23th ne gashi Yau its just 18,ita dai sam bata so tabar gidan

gashi ma ba acikin garin abuja za'ayi ba a kauyen da su hjya mamah suka taso ne..
Cikin tunanin ta sai tace toh meyesa tun ranar tafiya baiyi ba zaice naje gida?
...tace Toh nidai bazanje ko ina ba.

Haka tayi ta zaman ta bata gansa ba Kuwa gashi yanzu basu ko ga macici da Nimrah

, shikam Tun Yana mota zaije kano Ajiyan hjy tace masa ya bataga Su banafshn ba?
Yace mata Nimrah bata da lpya amma Banafsha zata zo

Yana isa kano Driver ya Kira ya aiko Akan yace mata maza ta shirya Ya kaita,Bata ma san baya garin ba

Gashi tsaban bata so taje ba da kuka ta fita Haraban gidan Da kayan ta

Nimrah ma farkawa tayi bata ganshi ba gashi bata san da maganan family function din ba Bare tafiyan dayayi.
,Daga tsayawar ta jikin window zata daura towel sai taji hayaniyan mai gadi da driver she tot ma ko mohan ne zai fita Baizo ya duba lpyar ta ba, tana kuwa lekowa ta hango ana dura kayan Banafsha a mota,

Ita kuma ta bata rai sai jijijiga babyn take agefe

wani Kyakyawan murmushi Nimrah tayi thinking that Mohan ne ya kore Ta duk Ba'a yadda taso Din ba .

Itama xaman jiran dawowar Sa take yaxo suci rayuwar su su kadai amma sai shiru har dare ya rufa,gashi zata kira shi bazai daga ba. .

Bai tashi kula ta ba sai chan dare yayi nisa anan ma"ya turo mata sakon cewa yayi tafiya zaikai 1 week bai dawo ba.

 Taji haushin haka Matuka Wai shi wani irin mutum ne Dabai damu da damuwar kowa ba? ,but tunda taga babu Banafsha a gidan bata wani daga hankali ba..

taso ace Ya kula da ita Wanka,cin abinci Abaki,Taga Dai yana lalubar ta akirjin sa kamar yadda yake yi ma Banafsha,amma Duk ina haka Nan take fama da kanta komai ita take yi makanta Ko mai aiki tayi

Kwana biyu kacal yayi a kano amma haka yake ganin miscals daga Wajen Banafsha da Nimrah wanda ko Daya baiya dagawa

..itako Banafsha tun data ga haka Sai ta kwallafa rai Akan Nimrah ce taja Hankalin sa yake kin daga wayar ta..

Gashi dama tunda taxo gida ta samu maysam na yawo tsakanin hjy mahnoor da su hjya Mamah sai Zama free ta kulla Tunanin mijin ta aranta..
..
A kwanan Sa na biyun Cikin dare sai taji ta kasa bacci tana ta juye juye,Ta rubuta ta goge chan kawai Sai ta tura Masa text Din"pls i want to talk to You"...

Yana gani yayi murmushi,dan shima baya iya runtsawa bata fado aranshi ba,duk da haka Sai da yaja aji after like 30minutes sai ya kira

,Ita kuwa tsaban rudani tunda ta tsaya rigiman tuno abunda zatace wayar ya yanke bai sake kira ba..
....
Da hawayen fushin hakan tayi bacci,da safe tana tashi tayi sallah Ko wanka batayi ba Ta Dura ma kanta yellow flagyll gadon hjy mamah ta dale tafashe da Wani sassaynr kukan makirci saida hankalin su ya tashi suka rufu kanta suna tambayr ta.

Baki Jin dadi ne tace Musu eh
Kuma lallai Yaya mohan ne xai duba ta Harda cewa ai magani Na wajen shi.

Tsoffin kam Haka Suka biye Mata,tunanin su ko dan tana cikin Inuwar jego har yanzu Bayason wani ya sa hannu akanta.
Tunda ta haihu sun san shikadai yake kula da lapyar ta

Don haka Kira akan kira,Banafsha Kuwa Sai ta haukace Musu Ta Zautar musu da tunani juya idanu Take acinyar hajy sai mashak mashak takeyi kamar mai Sabon laulayin ciki,Cikin ranta Kalau take jin kanta,"
sai tace wallhy sai kadawo Min Yau din nan, in har kana so na yau zan sani...

Haka su hjy Suka azizata magana saida hankalin shi ya tashi Ya kasa tabuka komai dake gaban sa....Gashi yana cikin mutane ne kasa kasa Ma yake maganan Na kusa da shi ma bai yaji

Yace Hjy nifa babu magani waje na',...hjya tace toh inma babu ai sai Ka dawo ka duba ta Yarinya tun safe jikin ta Ke ciwo kamar zata mutu Baga ganta ba abun tausayi,ko nabaka ita ne kaji da kunnen ka, Yace Ok bani ita.

Banafsha tunda taji haka Sai ta yi Boyayyen gyaran murya

Hjy na miko mata ta rufe kanta cikin bargo Dashi 2Sconds ya dauka yana jin wani munafukin numfashin ta a kunnen sa Jikin shi sai ya fara picturing masa Yanayin yadda Take a yanzun ,...Bayabo ba fallasa Yace what's wrong?Kince baki da lpya meke damun ki!?...Wani lumshe Ido mai ma'ana tayi Tana jin Shocking din Da muryan nasa Ya jona mata,

,"Itama Wani murya mai Shiga rai Ta Dasa mashi a kunne Wanda dadin sautin sa Ya sa shi mikewa tsaye Baisani ba
 Cikin sanyi Da janjanin kalma Tace Yaya nah katashi lpya?Tace..uhm dama zazzabi nake ji,Kuma ina rufe ido na sai Wani mafarki Yaxo min im so scared
..Tsoro nake ji Sosai Ko akwai maganin shi??

Jin yayi shiruu bai amsa ba Sai taji fargaban ko baiya ma jin ta ne Yayi shiru Din..

Bata san sigar datayi maganan bane ya girgiza zuciyan sa yabi ya razana gangan jikin Sa da shaukin kewar ta Ba"

"Bai iya Ko tsayawa acikin mutane ba Sai ya fita gefe jingine da bango ya lunshe idanun sa Yana sake boyayyan nishi..

Cikin yauqi tace yayah? Kanaji na
Har zai bude baki yace eh Sai yaji ya kasa

Wani Fitinannan kukan shagwaba Mai sanyi ta sake mishi a kunne Mai cakki da kuma yakushi Ajinin jiki,wanda
shikan sa Baya jin motsa motsan Data ke furtawa aciki..

Yo hjy mamah dake kusa da ita Ma bata jin ko A daga abunda suke cewa

Dik sai ta ruda shi 'cikin ransa sai yaji bazai iya kara dakikai bai ganta ba Cikin ranshi yace"ohhh this girl want to kill me softly,zata jefa bawan Allah cikin wani hali

 Karshen ta katse wayar yayi, A hujajan ya bar duk abunda yakeyin ta Jirgi Ma yabi ya diro garin abuja

Ita kuwa tinda taji baice komai ba ya kashe Wayar Sai ta ba hjy mamah abun ta Ta hade rai,Pillow ta matso kirjin ta ta bude Wani Sabon Shafin kuka,tun Shigar Mohan Jirgi bata dena ba sai da Taji muryan sa agidan

Gashi tsaban kukan datayi zazzabin gaske ne ya kama jikin ta Sosai ta hada dumi eye balls suka haura
 Hawayen ta shiga sharewa tana murmushi,
Yayi sallamah tare da Su hjy Maman ya shigo
Hjyn birni tace gata nan ko abinci fa bata ci ba..."Dukn su biyun sunyi Tsuru Tsuru suna tsaye

Shima tsaban zumudin daya cicciyo sa Sai Ya Zauna abakin gadon,bargon ya Dan yaye Kadan Yana kallon wani Dan iskan Kwanciyar da tayi

Don kuwa wani farin skin tight ta saka A yadda bai da kauri Har Ya hango Cewa ko pants bata sa Ba, Shikan sa kasa daga ido yayi ya kalli kirjin ta, Dan dunkule wa tayi kadan sai hannun ta suka matso cikakkun nonowar tan waje
..a lokacin jitake zuciyan ta dif dif Kamar zai buga tsaban fargaba bata iya motsi ba

,Sassanyar hannun shi da taji akan fore head Din ta Yasa ta bude lumsashun Idanun ta akansa Sunfi minti 5 a haka suna aika Ma juna wasu irin Wasu irin sakonni A tare yake ji haushin ta da kaunar ta a ransa..He just wonder why She changed"
What's wrong?Shikenan Hankalin ki ya kwanta kinsa nazo?sai yadan kamo ta Ta mike Kadan a Jikin sa,qamshin sa Ne ya dada bugar da ita Bata san sanda ta rungume shi ba,...
